الجزء ٣ الحزب ٥ ۞ تِلْكَ ٱلرُّسُلُ فَضَّلْنَا بَعْضَهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ مِّنْهُم مَّن كَلَّمَ ٱللَّهُ
وَرَفَعَ بَعْضَهُمْ دَرَجَٰتٍ وَءَاتَيْنَا عِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ ٱلْبَيِّنَٰتِ
وَأَيَّدْنَٰهُ بِرُوحِ ٱلْقُدُسِ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا ٱقْتَتَلَ ٱلَّذِينَ مِنۢ
بَعْدِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْهُمُ ٱلْبَيِّنَٰتُ وَلَٰكِنِ ٱخْتَلَفُوا۟
فَمِنْهُم مَّنْ ءَامَنَ وَمِنْهُم مَّن كَفَرَ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا ٱقْتَتَلُوا۟
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَفْعَلُ مَا يُرِيدُ ﴿٢٥٣﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَنفِقُوا۟
مِمَّا رَزَقْنَٰكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِىَ يَوْمٌ لَّا بَيْعٌ فِيهِ وَلَا خُلَّةٌ وَلَا
شَفَٰعَةٌ وَٱلْكَٰفِرُونَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٢٥٤﴾ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ
ٱلْحَىُّ ٱلْقَيُّومُ لَا تَأْخُذُهُۥ سِنَةٌ وَلَا نَوْمٌ لَّهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ مَن ذَا ٱلَّذِى يَشْفَعُ عِندَهُۥٓ إِلَّا بِإِذْنِهِۦ يَعْلَمُ
مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ وَلَا يُحِيطُونَ بِشَىْءٍ مِّنْ عِلْمِهِۦٓ إِلَّا
بِمَا شَآءَ وَسِعَ كُرْسِيُّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَلَا يَـُٔودُهُۥ حِفْظُهُمَا
وَهُوَ ٱلْعَلِىُّ ٱلْعَظِيمُ ﴿٢٥٥﴾ لَآ إِكْرَاهَ فِى ٱلدِّينِ قَد تَّبَيَّنَ ٱلرُّشْدُ مِنَ
ٱلْغَىِّ فَمَن يَكْفُرْ بِٱلطَّٰغُوتِ وَيُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱسْتَمْسَكَ
بِٱلْعُرْوَةِ ٱلْوُثْقَىٰ لَا ٱنفِصَامَ لَهَا وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٥٦﴾



**(253) Waxancan Manzanni da muka ambata maka su, mun fifita sashensu a kan sashe, a cikin wahayi da mabiya da darajoji, daga cikinsu akwai wanda Allah ya yi magana da shi, kamar Annabi Musa (A.S), daga cikinsu akwai wanda ya xaukaka darajoji maxaukaka, kamar Annabi Muhammad (S.A.W) yayin da aka aiko shi zuwa ga mutane gaba xaya, aka cika annabta da shi, aka fifita al'ummarsa a kan sauran al'ummu. Mun ba wa Annabi Isa xan Maryam mu'ujiza bayyananna, wadda take nuna annabcinsa, kamar raya matattu, da warkar da kutare, Muka qarfafa shi da mala'ika Jibrilu (A.S) don qarfafa shi a kan tsayuwa da umarnin Allah. Da Allah ya ga dama da waxanda suka zo bayan Manzanni ba su yi yaqi ba, bayan da ayoyi bayyanannu suka zo musu, sai dai sun sava, sun rabu gida biyu, daga cikinsu akwai waxanda suka yi imani da Allah, kuma akwai waxanda suka kafirce da shi. Da Allah ya ga damar kada su yi yaqi, da baza su yi yaqin ba, sai dai Allah yana aikata abin da ya yi nufi, ya shiryar da wanda ya so zuwa ga imani da rahamarsa da falalarsa, ya vatar da wanda ya ga dama da adalcinsa da hikimarsa. (254) Ya waxanda suka yi imani da Allah, su ka bi Manzonsa, ku ciyar daga abin da muka azurta ku da shi na halal, na dukiya daban-daban, tun gabanin ranar alqiyama ta zo, a wannan lokacin babu ciniki da mutum zai yi, ya samu abin da zai amfane shi, babu abota da zata amfani mutum a cikin wannan tsanani, babu wani tsani da zai kawar wa da mutum wata cuta, ko ya jawo masa wani amfani, sai dai idan Allah ya yi izini ga wanda ya so, kuma ya yarda da shi. Kafirai sune haqiqanin azzalumai, saboda kafirce wa Allah Maxaukakin Sarki da suka yi.**

**(255) Allah wanda babu wani abin bautawa bisa cancanta da gaskiya sai Shi, ba waninsa ba, wanda yake rayayye, rayuwa cikakkiya, wadda ba tawaya ko mutuwa a cikinta. Tsayayyen da ya tsaya da kansa, ya wadatu daga dukkan halittu. Da shi ne dukkan halittu suka tsaya, basa wadatuwa daga gare shi a kowane lokaci. Gyangyaxi ko barci basa kama shi, saboda cikar rayuwarsa da tsayuwarsa. Shi kaxai yake da mulkin abin da yake cikin sammai da qassai. Ba wanda ya mallaki ceto ga wani a wajensa, sai dai idan ya yi izini kuma ya yarda. Ya san abin da ya wuce na daga al'amuran halittarsa, daga cikin abin da ya faru, da abin da yake fuskantarsu daga abin da bai faru ba. Basu san komai daga iliminsa ba, sai abin da ya ga dama ya sanar da su. Kujerarsa – wurin digadigan Ubangiji - ta kewaye sammai da qassai duk da girmansu da faxinsu. Kiyaye su baya gajiyar da shi, ko ya yi masa wahala. Shi ne Maxaukaki da zatinsa da ikonsa da rinjayensa. Mai girma a cikin mulkinsa da ikonsa.**

**(256) Ba a tilastawa wani wajen shiga musulunci, saboda addinin gaskiya ne, bayyananne, baya buqatar a tilasta wani shiga cikinsa, shiriya ta bambanta da vata. Duk wanda ya kafirce wa dukkan abin da ake bautawa ba Allah ba, ya yi musu bara'a, ya yi imani da Allah shi kaxai, to ya yi riqo da igiya mai qarfi a cikin addini, wadda bata tsinkewa, don tsira ranar alqiyama. Allah yana jin maganganun bayinsa, ya san ayyukansu, kuma zai saka musu a kansu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Allah ya fifita tsakanin Manzanninsa da Annabawansa, wasu sun fi wasu falala, ya yi hakan ne da iliminsa da hikimarsa tsarki ya tabbata a gare shi. 2 - Tabbatar da siffar magana ga Allah Maxaukakin Sarki, a bisa yadda ya dace da girmansa. Kuma tabbas ya yi magana da wasu daga cikin Manzanninsa, kamar Annabi Musa, da Annabi Muhammad amincin Allah ya tabbata a gare su. 3 - Imani da shiriya da kafirci da vata dukkaninsu suna kasancewa ne da ganin damar Allah da qaddarawarsa. Allah yana da hikima cikakkiya, da ya ga dama da ya shiryar da dukkan halittu gaba xaya. 4 - Ayatul-Kursiyyi ita ce mafi girman aya a littafin Allah, saboda abin da ta qunsa na ayyukan Allah da bautarsa da bayanin siffofinsa, mai girma da buwaya. 5 - Karvar musulunci da shiga cikinsa wajibi ne ya zama a bisa amincewa, da karvar abin da ya zo da shi. Babu tilas a cikin addinin Allah Maxaukakin Sarki. 6 - Riqo da littafin Allah, da sunnar Manzonsa, su ne mafi girman hanyar samun arziqi a duniya, da rabauta a lahira.**

ٱللَّهُ وَلِيُّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ يُخْرِجُهُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ ۖ
وَٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ أَوْلِيَآؤُهُمُ ٱلطَّٰغُوتُ يُخْرِجُونَهُم مِّنَ
ٱلنُّورِ إِلَى ٱلظُّلُمَٰتِ ۗ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ ۖ هُمْ فِيهَا
خَٰلِدُونَ ﴿٢٥٧﴾ أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِى حَآجَّ إِبْرَٰهِۦمَ فِى رَبِّهِۦٓ
أَنْ ءَاتَىٰهُ ٱللَّهُ ٱلْمُلْكَ إِذْ قَالَ إِبْرَٰهِۦمُ رَبِّىَ ٱلَّذِى يُحْىِۦ
وَيُمِيتُ قَالَ أَنَا۠ أُحْىِۦ وَأُمِيتُ ۖ قَالَ إِبْرَٰهِۦمُ فَإِنَّ ٱللَّهَ يَأْتِى
بِٱلشَّمْسِ مِنَ ٱلْمَشْرِقِ فَأْتِ بِهَا مِنَ ٱلْمَغْرِبِ فَبُهِتَ ٱلَّذِى
كَفَرَ ۗ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٢٥٨﴾ أَوْ كَٱلَّذِى
مَرَّ عَلَىٰ قَرْيَةٍ وَهِىَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا قَالَ أَنَّىٰ يُحْىِۦ
هَٰذِهِ ٱللَّهُ بَعْدَ مَوْتِهَا ۖ فَأَمَاتَهُ ٱللَّهُ مِا۟ئَةَ عَامٍ ثُمَّ بَعَثَهُۥ ۖ
قَالَ كَمْ لَبِثْتَ ۖ قَالَ لَبِثْتُ يَوْمًا أَوْ بَعْضَ يَوْمٍ ۖ قَالَ بَل
لَّبِثْتَ مِا۟ئَةَ عَامٍ فَٱنظُرْ إِلَىٰ طَعَامِكَ وَشَرَابِكَ لَمْ يَتَسَنَّهْ ۖ
وَٱنظُرْ إِلَىٰ حِمَارِكَ وَلِنَجْعَلَكَ ءَايَةً لِّلنَّاسِ ۖ وَٱنظُرْ إِلَى
ٱلْعِظَامِ كَيْفَ نُنشِزُهَا ثُمَّ نَكْسُوهَا لَحْمًا ۚ فَلَمَّا
تَبَيَّنَ لَهُۥ قَالَ أَعْلَمُ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢٥٩﴾



(257) Allah yana jivintar waxanda suka yi imani da shi, yana datar da su, yana ba su nasara, yana fitar da su daga duhun kafirci da jahilci zuwa hasken imani da ilimi. Waxanda suka kafirta kuwa majivintansu sune gumaka, waxanda suka qawata musu kafirci, suka fitar da su daga hasken imani da ilimi, zuwa duhun kafirci da jahilci. Waxannan sune ma’abota wuta, zasu zauna a cikinta har abada.

Bayan Allah ya faxi vangarorin biyu, sai ya buga misalai guda biyu, ya ce:

(258) Shin ya kai wannan Annabi ko ka ga abin mamaki, wanda ya fi qarfin halin da wani mai xagawa ya nuna, wanda ya yi jayayya da Annabi Ibrahim (A.S) a kan ayyukan Allah da kaxaita shi da bauta, kuma ya yi hakan ne, don Allah ya ba shi mulki, shi ya sa ya yi xagawa, yayin da Annabi Ibrahim ya bayyana masa siffofin Allah ya ce masa: “Ubangijina yana raya halitta, kuma yana kashe su”. Sai wannan mai xagawar ya ce: “Ni ma ina rayawa, ina kuma kashewa”, shi ne ya kashe wanda ya ga dama, ya yi afuwa ga wanda ya ga dama. Sai Annabi Ibrahim ya fito masa da wata hujja mai qarfi, kuma mai girma, ya ce da shi: “Ubangijina wanda nake bautawa, yana zuwa da rana daga inda take fitowa, to kai ka zo da ita daga inda take faxuwa”. Sai wannan mai xagawa ya ruxe ya rasa mai zai ce, aka rinjaye shi da qarfin hujja. Allah baya datar da azzalumai zuwa ga bin hanya, saboda xagawarsu da zaluncinsu.

(259) Ko ka ga misalin wanda ya wuce ta wajen wata Alqarya, rufin gidajenta ya faxo qasa, katangunta sun rushe, mazauna garin sun halaka, ya zama babu kowa, abun abin tsoro. Sai wannan mutumin ya yi mamaki, ya ce,: “Ta yaya Allah zai raya mutanen wannan alqarya bayan mutuwarsu?!”. Sai Allah ya kashe shi tsawon shekara xari, sannan sai ya raya shi, ya tambaye shi, ya ce da shi: “Shekara nawa ka yi a mace?” Sai ya ba da amsa ya ce: “Na zauna yini xaya ko sashen yini”. Sai ya ce da shi, “A’a ka zauna tsawon shekara xari ne. kalli abin da yake tare da kai na abinci da abin sha, ga shi nan yadda yake bai canza ba, duk da cewa ba abin da ya fi abinci saurin lalacewa. Kalli mataccen jakinka, hakan ya faru ne, ka zama alama bayananniya ga mutane wadda take nuna ikon Allah a kan tashinsu. Kalli qasusuwan jakinka waxanda suka rabu da juna, suka xaixaice, yaya muke xaga su, muke haxa sashensu zuwa ga sashe, sannan mu lulluve su da nama, mu dawo musu zuwa ga rayuwa”. Da ya ga haka, sai haqiqanin lamarin ya bayyana a gare shi, ya gane ikon Allah, ya ce – yana mai tabbatar da hakan – “Na sani haqiqa Allah mai iko ne a kan dukkan komai”.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Babban abin da masu imani suka bambanta da shi, shi ne su, suna kan shiriya da basira daga wajen Allah a cikin dukkan lamuransu na addini da na duniya, savanin kafirai.

2 - Daga mafi girman abin da yake sa xagawa, ruxuwa da qarfi da iko, har mutum ya makance daga haqiqanin halinsa.

3 - Halaccin tattaunawa da mavarnata don fito da gaskiya, da bayyana vata daga shiriya.

4 - Girman ikon Allah. Babu wani abin da ya gagare shi, har raya matattu.

وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِـۧمُ رَبِّ أَرِنِي كَيْفَ تُحْيِ ٱلْمَوْتَىٰۖ قَالَ أَوَلَمْ
تُؤْمِنۖ قَالَ بَلَىٰ وَلَٰكِن لِّيَطْمَئِنَّ قَلْبِيۖ قَالَ فَخُذْ أَرْبَعَةً مِّنَ
ٱلطَّيْرِ فَصُرْهُنَّ إِلَيْكَ ثُمَّ ٱجْعَلْ عَلَىٰ كُلِّ جَبَلٍ مِّنْهُنَّ جُزْءًا
ثُمَّ ٱدْعُهُنَّ يَأْتِينَكَ سَعْيًاۚ وَٱعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ
٢٦٠ مَّثَلُ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَٰلَهُمْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ كَمَثَلِ حَبَّةٍ
أَنۢبَتَتْ سَبْعَ سَنَابِلَ فِي كُلِّ سُنۢبُلَةٍ مِّاْئَةُ حَبَّةٍۗ وَٱللَّهُ
يُضَٰعِفُ لِمَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ٢٦١ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ
أَمْوَٰلَهُمْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ ثُمَّ لَا يُتْبِعُونَ مَآ أَنفَقُواْ مَنًّا وَلَآ
أَذًى لَّهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ
يَحْزَنُونَ ٢٦٢ ۞ قَوْلٌ مَّعْرُوفٌ وَمَغْفِرَةٌ خَيْرٌ مِّن صَدَقَةٍ (ربع الحزب)
يَتْبَعُهَآ أَذًىۗ وَٱللَّهُ غَنِيٌّ حَلِيمٌ ٢٦٣ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
لَا تُبْطِلُواْ صَدَقَٰتِكُم بِٱلْمَنِّ وَٱلْأَذَىٰ كَٱلَّذِي يُنفِقُ مَالَهُۥ
رِئَآءَ ٱلنَّاسِ وَلَا يُؤْمِنُ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْأٓخِرِۖ فَمَثَلُهُۥ كَمَثَلِ
صَفْوَانٍ عَلَيْهِ تُرَابٌ فَأَصَابَهُۥ وَابِلٌ فَتَرَكَهُۥ صَلْدًاۖ لَّا يَقْدِرُونَ
عَلَىٰ شَيْءٍ مِّمَّا كَسَبُواْۗ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِي ٱلْقَوْمَ ٱلْكَٰفِرِينَ ٢٦٤



**(260) Ka tuna – Ya kai wannan Annabi – yayin da Annabi Ibrahim (A.S) ya ce,: "Ya Ubangiji ka nuna min da idona yaya kake raya matattu!". Sai Allah ya ce da shi: "Ashe baka yi imani da wannan lamarin ba?" Sai Annabi Ibrahim ya ce: "A'a tabbas na yi imani, sai dai don qarin samun nutsuwa a zuciyata", sai Allah ya umarce shi, ya ce da shi: "Ka xauki tsuntsaye guda huxu, ka haxa su, ka yan yanka su, sannan ka sa a kan kowane dutse da yake kusa da kai, wani yanki na tsuntsayen, sannan sai ka kira su, zasu zo maka suna gaggawa, rayuwa da dawo musu. Ka sani – Ya Ibrahim – haqiqa Allah Mabuwayi ne a cikin mulkinsa, mai hikima ne a cikin lamarinsa da shari'arsa da halittarsa".**

**(261) Misalin ladan muminan da suke ciyar da dukiyoyinsu saboda Allah, kamar qwaya ce, wadda mai shuka yake sa wa a cikin qasa mai kyau, sai ta fitar da zangarniya bakwai, a cikin kowace zangarniya akwai qwaya xari. Allah yana ninninka lada ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa. Ya ba su lada ba tare da hisabi ba. Allah mai yalwar falala ne da bayarwa, ya san wanda ya cancanta a ninninkawa.**

**(262) Waxanda suke ba da dukiyoyinsu a cikin xa'ar Allah da neman yardarsa, sannan ba sa biyo baya da abin da zai vata ladansu na gori ga mutane, ko da baki ko da aiki, suna da ladansu a wurin Ubangijinsu. Babu tsoro a kansu cikin abin da suke fuskanta, babu baqin ciki a kan abin da ya wuce su, saboda girman ni'imarsu.**

**(263) Magana mai girma, wadda take shigar da farin ciki a zuciyar mumini, da afuwa ga wanda ya munana, ya fi falala daga sadakar da cutar da wanda aka ba sadakar yake biyo bayanta. Allah Mawadaci ne ga barin bayinsa, mai haquri, ba ya gaggauta musu uquba.**

**(264) Ya waxanda suka yi imani da Allah, suka bi Manzonsa, kada ku vata ladan sadakarku da yi wa wanda aka ba sadaka gori da cutar da shi. Misalin wanda yake yin haka, kamar misalin wanda yake ba da dukiyarsa ne don mutane su gani, su yabe shi, alhali shi kafiri ne bai yi imani da Allah da ranar lahira ba, da abin da yake cikinta na lada da azaba. Misalin wannan kamar dutsen kamfa ne, a saman shi da turvaya, sai ruwa mai yawa ya samu wannan dutsen, ya kawar da wannan turvayar daga kan dutsen, ya bar shi babu komai a kansa. To hakanan masu riya, ladan ayyukansu da ciyarwarsu yana tafiya, babu abin da yake saura a wurin Allah. Allah baya shiryar da kafirai zuwa ga abin da ya yarda da shi, wanda zai amfane su a cikin ayyukansu da ciyarwarsu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Matakan imani da Allah da matakan masu yaqini da shi, matakai-matakai ne ba su da iyaka, a duk lokacin da bawa ya qara duba ayoyin Allah da ya saukar da waxanda ya halitta, sai ya qara imani da yaqini.**

**2 - Tashin da Allah zai yi wa bayi bayan mutuwarsu dalili ne bayyananne dake nuna cikar ikonsa da cikar girmansa, tsarki ya tabbata a gare shi.**

**3 - Falalar ciyarwa a tafarkin Allah, da girman ladan hakan, idan aka samu niyya tagari, kuma cuta ko gori waxanda suke rusa ayyuka ba su biyo baya ba.**

**4 - Yana daga mafi kyan abin da mutum zai gabatarwa mutane kyawawan halaye, a magana ko aiki mai kyau, da yi wa wanda ya munana masa afuwa.**

وَمَثَلُ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمۡوَٰلَهُمُ ٱبۡتِغَآءَ مَرۡضَاتِ ٱللَّهِ
وَتَثۡبِيتٗا مِّنۡ أَنفُسِهِمۡ كَمَثَلِ جَنَّةِۭ بِرَبۡوَةٍ أَصَابَهَا وَابِلٞ
فَـَٔاتَتۡ أُكُلَهَا ضِعۡفَيۡنِ فَإِن لَّمۡ يُصِبۡهَا وَابِلٞ فَطَلّٞۗ
وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٌ ٢٦٥ أَيَوَدُّ أَحَدُكُمۡ أَن تَكُونَ لَهُۥ
جَنَّةٞ مِّن نَّخِيلٖ وَأَعۡنَابٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ لَهُۥ
فِيهَا مِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ وَأَصَابَهُ ٱلۡكِبَرُ وَلَهُۥ ذُرِّيَّةٞ
ضُعَفَآءُ فَأَصَابَهَآ إِعۡصَارٞ فِيهِ نَارٞ فَٱحۡتَرَقَتۡۗ كَذَٰلِكَ
يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّكُمۡ تَتَفَكَّرُونَ ٢٦٦ يَـٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنفِقُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا كَسَبۡتُمۡ وَمِمَّآ أَخۡرَجۡنَا
لَكُم مِّنَ ٱلۡأَرۡضِۖ وَلَا تَيَمَّمُواْ ٱلۡخَبِيثَ مِنۡهُ تُنفِقُونَ
وَلَسۡتُم بِـَٔاخِذِيهِ إِلَّآ أَن تُغۡمِضُواْ فِيهِۚ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ غَنِيٌّ
حَمِيدٌ ٢٦٧ ٱلشَّيۡطَٰنُ يَعِدُكُمُ ٱلۡفَقۡرَ وَيَأۡمُرُكُم بِٱلۡفَحۡشَآءِۖ
وَٱللَّهُ يَعِدُكُم مَّغۡفِرَةٗ مِّنۡهُ وَفَضۡلٗاۗ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٞ
٢٦٨ يُؤۡتِي ٱلۡحِكۡمَةَ مَن يَشَآءُۚ وَمَن يُؤۡتَ ٱلۡحِكۡمَةَ فَقَدۡ
أُوتِيَ خَيۡرٗا كَثِيرٗاۗ وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّآ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٢٦٩



**265 Misalin muminan da suke ba da dukiyarsu don neman yardar Allah, da nutsuwa a cikin zukatansu a kan gaskiyar alqawarin Allah da ya yi musu, basu bayar ba suna qi a zuciyarsu, kamar wata gona ce da take wani wuri mai kyau a tudu, mamakon ruwan sama ya same ta, ta fitar da yayan itace ninkin- ba ninkin, idan mamakon ruwa bai same ta ba, sai xan kaxan ne ya sauka a cikinta, kuma ya wadace ta, saboda kyan qasar wurin, to haka ciyarwar masu tsarkake zukatansu take a wurin Allah, yana karvarta, ya ninninka ladanta, koda kuwa kaxan ce. Allah yana ganin abin da kuke aikatawa, halin masu tsarkake zuciyarsu da waxanda suke riya ba ya vuya a gare shi, zai sakawa kowa da abin da ya cancanta. Sannan sai Allah ya buga wani misalin, na halin wanda yake ciyar da dukiyarsa don riya. Ya ce:**

**266 Yanzu xayanku zai so a ce yana da lambu, a cikinsa akwai dabinai da inabi, ga ruwa mai daxi yana gudana a qarqashinta, kuma a cikinta akwai dukkan kayan marmari masu daxi, sai girma ya same shi, ya zama tsoho baya iya noma komai ko aiki, sannan ga shi yana da 'ya'ya qanana masu rauni, basu iya aiki ba, sannan iska mai tsanani da wuta a cikinta ta faxawa lambun, ya qone gaba xaya, a lokacin da ya fi kowane lokaci buqatarsa, saboda tsufansa da raunin zuriyarsa!. Yanzu a cikinku, akwai mai son haka?. To wanda yake ciyar da dukiyarsa don riya, halinsa kamar halin wannan mutumin ne, zai je wajen Allah ranar alqiyama ba tare da wasu kyawawan ayyuka ba, a lokacin da yake da tsananin buqatarsu. Irin wannan bayanin, na abin da zai amfane ku a duniya da lahira, Allah yake yi muku, ko kwa yi tunani a cikinsa.**

**267 Ya waxanda suka yi imani da Allah, suka bi Manzonsa, ku ciyar da dukiyarku ta halal, na daga abin da kuka tsururuta. Haka nan ku ciyar daga abin da muka fitar muku daga tsirran bayan qasa. Kada ku nufi vataccen abu daga cikinsa, ku ce a cikinsa zaku ciyar, abin da, da za a baku shi, baza ku karve shi ba, cikin jin daxi, sai dai a dole, saboda rashin kyansa. To ta yaya za ku yarda ku ba Allah abin da ku ma baku yarda da shi ba?!. Ku sani Allah Mawadaci ne ga barin abin da kuke ciyarwa, Allah ne abin godiya a zatinsa da ayyukansa.**

**Yayin da ya umarce su da ciyar da mai kyau, sai ya tsoratar da su daga makircin Shaixan da wasi-wasinsa, Ya ce:**

**268 Shaixan yana tsoratar da ku da talauci, yana kwaxaitar da ku yin rowa, yana kiranku zuwa yin laifuka da zunubai. Allah kuma yana muku alqawarin wata gafara mai girma daga zunubanku, da arziki mai yalwa. Allah mai yalwar falala ne, kuma masani ne na halin bayinsa.**

**269 Yana ba wa wanda ya ga dama daga cikin bayinsa dacewa a magana, da yin daidai a cikin ayyuka. Duk wanda aka ba wa haka, to haqiqa an ba shi alheri mai yawa. Ba wanda yake wa'azantuwa da gargaxuwa da ayoyin Allah sai masu hankali cikakke, waxanda suke haskuwa da shi, suke shiriya da shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Waxanda suka yi imani da Allah da gaske, suna da tabbacin alqawarin Allah da ladansa, suna ciyar da dukiyoyinsu, ba tare da tsoro ko baqin ciki ba, ko juyawa zuwa ga wasiwasin Shaixan ba, da irin tsoratarwa da talauci da buqata da yake yi musu.**

**2 - Tsarkake niyya yana daga cikin manya-manyan abin da ayyuka suke samun albarka da havaka da shi.**

**3 - Wanda ya fi kowa halaka a cikin mutane shi ne wanda yake riya da ayyukansa, saboda bai da ladan aikinsa sai yabon mutane.**

وَمَآ أَنفَقْتُم مِّن نَّفَقَةٍ أَوْ نَذَرْتُم مِّن نَّذْرٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ
يَعْلَمُهُۥ ۗ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ أَنصَارٍ ٢٧٠ إِن تُبْدُوا۟
ٱلصَّدَقَٰتِ فَنِعِمَّا هِىَ ۖ وَإِن تُخْفُوهَا وَتُؤْتُوهَا
ٱلْفُقَرَآءَ فَهُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ ۚ وَيُكَفِّرُ عَنكُم مِّن
سَيِّـَٔاتِكُمْ ۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ٢٧١ ۞ لَّيْسَ نصف الحزب ٥
عَلَيْكَ هُدَىٰهُمْ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَهْدِى مَن يَشَآءُ ۗ وَمَا
تُنفِقُوا۟ مِنْ خَيْرٍ فَلِأَنفُسِكُمْ ۚ وَمَا تُنفِقُونَ إِلَّا
ٱبْتِغَآءَ وَجْهِ ٱللَّهِ ۚ وَمَا تُنفِقُوا۟ مِنْ خَيْرٍ يُوَفَّ إِلَيْكُمْ
وَأَنتُمْ لَا تُظْلَمُونَ ٢٧٢ لِلْفُقَرَآءِ ٱلَّذِينَ أُحْصِرُوا۟
فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ لَا يَسْتَطِيعُونَ ضَرْبًا فِى ٱلْأَرْضِ
يَحْسَبُهُمُ ٱلْجَاهِلُ أَغْنِيَآءَ مِنَ ٱلتَّعَفُّفِ تَعْرِفُهُم
بِسِيمَٰهُمْ لَا يَسْـَٔلُونَ ٱلنَّاسَ إِلْحَافًا ۗ وَمَا تُنفِقُوا۟ مِنْ
خَيْرٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ بِهِۦ عَلِيمٌ ٢٧٣ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَٰلَهُم
بِٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ سِرًّا وَعَلَانِيَةً فَلَهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ
رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ٢٧٤



**270 Duk abin da kuka ciyar na ciyarwa, kaxan ne ko da yawa, don neman yardar Allah, ko kuka lazimci aikin xa'a na ganin dama, wanda ba a xora muku ba, to Allah ya san wannan duka, kuma babu abin da zai tozarta a wurinsa, zai saka muku a kanshi, da mafi girman sakamako. Azzalumai waxanda suka hana abin da ya wajaba a kansu, masu qetare iyakokin Allah, ba su da mataimaka da za su kawar musu da azaba ranar alqiyama.**

**271 Idan kuka bayyana abin da kuke bayarwa na sadakar dukiyarku, to madalla da sadakarku, idan kuka voye ta, kuka ba wa talakawa, to hakan shi ya fi alheri gare ku fiye da bayyanawar, saboda hakan ya fi kusa da tsarkake zuciya. A cikin sadakar masu tsarkake zuciyarsu akwai gafara ga zunubai da rufe su. Allah Masani ne, mai ba da labarin abin da kuke aikatawa, babu wani abin da zai vuya gare shi daga cikin halayenku.**

**272 Shiriyarsu zuwa ga karvar gaskiya da bin ta, da tilasta musu hakan, baya kanka – Ya kai wannan Annabi -. Kaxai abin da ya wajaba a kanka shi ne nuna musu gaskiya da sanar da su ita. Amma dacewa da shiriya zuwa ga gaskiya yana hannun Allah, Shi ne yake shiryar da wanda ya ga dama. Duk abin da kuka ciyar na alheri to amfaninsa zai dawo zuwa gareku, saboda Allah Mawadaci ne daga gareku, don haka ku ciyar saboda Allah. Muminai na gaskiya basa ciyarwa sai don neman yardar Allah. Duk abin da kuka ciyar na alheri, kaxan ne ko da yawa, to za a baku ladansa cikakke ba tare da an rage ba, saboda Allah ba ya zaluntar kowa.**

**Da Allah ya ambaci ciyarwa akan tafarkinsa, ya kuma kira muminai zuwa ga hakan, sannan ya bayyana musu inda za su ciyar da dukiyar, Ya ce:**

**273 Ku bayar da ita ga talakawa, waxanda jihadi a kan tafarkin Allah ya hana su tafiya neman arziki. Wanda bai sani ba yana zaton su mawadata ne, saboda sun kame, basa roqo, wanda kuma ya san lamarinsu yana gane su da alamominsu, na bayyanar buqata a jikinsu da tufafinsu. Daga cikin siffofinsu ba daidai suke da talakawa ba, waxanda suke roqon mutane, suna naci a wajen roqonsu. Duk abin da kuka ciyar na dukiya da wanin ta to haqiqa Allah ya san shi, kuma zai saka muku da mafi girman sakamako.**

**274 Waxanda suke ciyar da dukiyoyinsu don neman yardar Allah, dare da rana, a fili da voye, ba don a gani, ko don aji labari ba, to suna da ladansu a wajen Ubangijinsu ranar alqiyama. Babu tsoro a kansu cikin abin da suke fuskanta, babu baqin ciki a tare da su a kan abin da ya wuce su a duniya, saboda falalar Allah da ni'imarsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Idan mumini ya tsarkake niyyarsa a wajen ciyarwarsa da sadaka to babu laifi ya bayyana ta, ko ya voye ta, gwargwadon maslaha, duk da cewa voyewar ya fi girman lada, saboda ya fi kusa da yi don Allah.**

**2 - Kiran muminai zuwa ga waiwayawa da kula da mabuqata, waxanda kamewa ta hana su bayyana halin da suke ciki, da roqon mutane.**

**3 - Halaccin ciyarwa saboda Allah a kowane lokaci da yanayi, da girman ladanta, saboda Allah ya yi alqawarin lada mai girma a duniya da lahira a kanta.**

ٱلَّذِينَ يَأۡكُلُونَ ٱلرِّبَوٰاْ لَا يَقُومُونَ إِلَّا كَمَا يَقُومُ ٱلَّذِي
يَتَخَبَّطُهُ ٱلشَّيۡطَٰنُ مِنَ ٱلۡمَسِّۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَالُوٓاْ إِنَّمَا ٱلۡبَيۡعُ
مِثۡلُ ٱلرِّبَوٰاْۗ وَأَحَلَّ ٱللَّهُ ٱلۡبَيۡعَ وَحَرَّمَ ٱلرِّبَوٰاْۚ فَمَن جَآءَهُۥ
مَوۡعِظَةٞ مِّن رَّبِّهِۦ فَٱنتَهَىٰ فَلَهُۥ مَا سَلَفَ وَأَمۡرُهُۥٓ إِلَى ٱللَّهِۖ وَمَنۡ
عَادَ فَأُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٢٧٥ يَمۡحَقُ
ٱللَّهُ ٱلرِّبَوٰاْ وَيُرۡبِي ٱلصَّدَقَٰتِۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ كُلَّ كَفَّارٍ أَثِيمٍ
٢٧٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ
وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ لَهُمۡ أَجۡرُهُمۡ عِندَ رَبِّهِمۡ وَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ
وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ٢٧٧ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ
وَذَرُواْ مَا بَقِيَ مِنَ ٱلرِّبَوٰٓاْ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٢٧٨ فَإِن لَّمۡ تَفۡعَلُواْ
فَأۡذَنُواْ بِحَرۡبٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦۖ وَإِن تُبۡتُمۡ فَلَكُمۡ رُءُوسُ
أَمۡوَٰلِكُمۡ لَا تَظۡلِمُونَ وَلَا تُظۡلَمُونَ ٢٧٩ وَإِن كَانَ
ذُو عُسۡرَةٖ فَنَظِرَةٌ إِلَىٰ مَيۡسَرَةٖۚ وَأَن تَصَدَّقُواْ خَيۡرٞ لَّكُمۡ
إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٢٨٠ وَٱتَّقُواْ يَوۡمٗا تُرۡجَعُونَ فِيهِ إِلَى
ٱللَّهِۖ ثُمَّ تُوَفَّىٰ كُلُّ نَفۡسٖ مَّا كَسَبَتۡ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ٢٨١



**Da Allah ya kwaxaitar a kan ciyarwa a bisa tafarkinsa, saboda abin da yake cikin hakan na taimakon juna a tsakanin musulmi, sai kuma ya tsawatar daga abin da yake warware hakan, shi ne cin riba. Ya ce: (275) Waxanda suke mu'amala da riba, suke karvarta, basa tashi daga qaburburansu ranar alqiyama sai kamar yadda wanda yake da shafar Shaixan yake tashi. Zai tashi a cikin qabarinsa yana buge-buge kamar yadda wanda yake da farfaxiya yake yi, yayin tashinsa ko faxuwarsa, saboda sun halatta cin riba, ba su bambance tsakanin riba da abin da Allah ya halatta ba na cinikayya, suka ce: Ai ciniki kamar riba yake wajen halacci, saboda kowannensu yana qara dukiya da havaka ta. Sai Allah ya yi musu raddi, ya nuna qiyasin da suka yi vatacce ne, ya qaryata su, ya bayyana cewa Allah Maxaukakin Sarki ya hallata ciniki saboda abin da yake cikinsa na amfani kevantacce ko gamamme, ya kuma haramta riba saboda abin da yake cikinta na cin dukiyar mutane da varna ko a banza. Duk wanda wa'azi ya zo masa daga Ubangijinsa, wanda a cikinsa akwai hani da tsoratarwa daga riba, ya hanu, ya tuba zuwa ga Allah, to abin da ya riga ya karva na daga riba to na shi ne, babu laifi a kansa, lamarinsa yana ga Allah cikin abin da zai yi gaba. Wanda duk ya koma zuwa ga karvar riba, bayan hani ya zo masa daga Allah, hujja ta tsaya a kansa, to ya cancanci shiga wuta, wanda ake daxe wa a cikinta, domin dauwama a cikin wuta sai waxanda suke kafirai. Amma masu kaxaita Allah (tauhidi) ba za su dauwama a cikinta ba. Da Allah ya ambaci ciyarwa a kan tafarkinsa, da hana karvar riba, sai Allah ya bayyana bambancinsu a wajen sakamako, Ya ce: (276) Allah yana halakar da dukiyar riba, ya tafiyar da ita, kodai a zahiri ta hanyar lalatata, ko makamancin haka, ko kuma ba a zahiri ba, ta hanyar cire mata albarka, amma kuma yana qara sadaka, ya havaka ta, ya ninninka ladanta, kyakkyawa xaya daidai take da goma irinta, zuwa ninki xari bakwai, zuwa ninki da yawa. Yana sa albarka a dukiyar masu sadaka. Allah baya son wanda yake kafiri mai taurin kai, mai halatta haram, mai ci gaba da savo da zunubi. (277) Waxanda suka yi imani da Allah, suka bi Manzonsa, suka yi ayyuka nagari, suka yi sallah cikakkiya kamar yadda aka shar'anta, suka ba da zakkar dukiyoyinsu ga wanda ya cancanta, to ladansu yana wajen Ubangijinsu. Babu tsoro a kansu cikin abin da suke fuskanta, kuma ba za su yi baqin ciki ba na abin da ya wuce su a duniya na ni'imarta. (278) Ya waxanda suka yi imani da Allah, suka bi Manzonsa, ku ji tsoron Allah, ku kamanta abin da ya yi umarni da shi, ku nisanci abubuwan da ya hana, ku bar neman abin da ya rage muku na dukiyar riba da take wajen mutane, in dai kun yi imani da Allah na gaskiya, kun yi imani da abin da ya hana ku na riba. (279) Idan kuwa baku aikata abin da aka umarceku ba, to ku sani, ku tabbatar da yaqi daga wajen Allah da Manzonsa. Idan kuka tuba kuka bar riba, to kuna da damar ku karvi iya abin da kuka bada bashi daga dukiyoyinku, ba tare da kun zalinci wani ba, ta hanyar karvar qari a kan abin da kuka bayar na dukiyarku ba, kuma ba a zalunce ku ba, ta hanyar rage muku dukiyar. (280) Idan wanda kuke nema da ya biya bashin da kuke bin sa yana cikin matsi, bai da abin da zai biya bashin da shi, to ku jinkirta neman biyan bashin zuwa lokacin da dukiyar ta sauwaka a gare shi, ya samu abin da zai biya ku da shi. Yi masa sadaka, da qyale masa bashin, ko rage masa ya fi alheri a kanku, da kun san falalar hakan a wurin Allah Maxaukakin Sarki. (281) Ku ji tsoron azabar wata rana da zaku koma gaba xayanku zuwa ga Allah a cikinta, za ku tsaya a gabansa, sannan a ba wa kowace rai sakamakon abin da ta aikata na alheri ko sharri. Ba za a zalunce ku ba da rage muku ladan kyawawan ayyukanku, ba kuma za a qara muka azaba a kan laifukanku ba.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Yana daga manya-manyan zunubai cin riba, don haka ma Allah ya yi wa mai cin ta alqawarin yaqi da shafe albarka a duniya, da kuma buge-buge irin na mai ciwon farfaxiya a lahira. 2 - Lazimtar hukunce-hukuncen shari'a a cikin mu'amalar dukiya, yana saukar da albarka da havaka a cikinta.**
**3 - Falalar haquri ga wanda yake cikin matsi, da saukaka masa, ta hanyar yi masa sadaka da wani sashe na bashin ko gaba xayansa.**

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا تَدَايَنتُم بِدَيۡنٍ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى
فَٱكۡتُبُوهُۚ وَلۡيَكۡتُب بَّيۡنَكُمۡ كَاتِبُۢ بِٱلۡعَدۡلِۚ وَلَا يَأۡبَ
كَاتِبٌ أَن يَكۡتُبَ كَمَا عَلَّمَهُ ٱللَّهُۚ فَلۡيَكۡتُبۡ وَلۡيُمۡلِلِ
ٱلَّذِي عَلَيۡهِ ٱلۡحَقُّ وَلۡيَتَّقِ ٱللَّهَ رَبَّهُۥ وَلَا يَبۡخَسۡ مِنۡهُ شَيۡـٔٗاۚ
فَإِن كَانَ ٱلَّذِي عَلَيۡهِ ٱلۡحَقُّ سَفِيهًا أَوۡ ضَعِيفًا أَوۡ لَا يَسۡتَطِيعُ
أَن يُمِلَّ هُوَ فَلۡيُمۡلِلۡ وَلِيُّهُۥ بِٱلۡعَدۡلِۚ وَٱسۡتَشۡهِدُواْ شَهِيدَيۡنِ
مِن رِّجَالِكُمۡۖ فَإِن لَّمۡ يَكُونَا رَجُلَيۡنِ فَرَجُلٞ وَٱمۡرَأَتَانِ
مِمَّن تَرۡضَوۡنَ مِنَ ٱلشُّهَدَآءِ أَن تَضِلَّ إِحۡدَىٰهُمَا فَتُذَكِّرَ
إِحۡدَىٰهُمَا ٱلۡأُخۡرَىٰۚ وَلَا يَأۡبَ ٱلشُّهَدَآءُ إِذَا مَا دُعُواْۚ وَلَا تَسۡـَٔمُوٓاْ
أَن تَكۡتُبُوهُ صَغِيرًا أَوۡ كَبِيرًا إِلَىٰٓ أَجَلِهِۦۚ ذَٰلِكُمۡ أَقۡسَطُ
عِندَ ٱللَّهِ وَأَقۡوَمُ لِلشَّهَٰدَةِ وَأَدۡنَىٰٓ أَلَّا تَرۡتَابُوٓاْ إِلَّآ أَن تَكُونَ
تِجَٰرَةً حَاضِرَةٗ تُدِيرُونَهَا بَيۡنَكُمۡ فَلَيۡسَ عَلَيۡكُمۡ جُنَاحٌ
أَلَّا تَكۡتُبُوهَاۗ وَأَشۡهِدُوٓاْ إِذَا تَبَايَعۡتُمۡۚ وَلَا يُضَآرَّ كَاتِبٞ
وَلَا شَهِيدٞۚ وَإِن تَفۡعَلُواْ فَإِنَّهُۥ فُسُوقُۢ بِكُمۡۗ وَٱتَّقُواْ
ٱللَّهَۖ وَيُعَلِّمُكُمُ ٱللَّهُۗ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ٢٨٢



**282 Ya waxanda suka yi imani da Allah, suka bi Manzonsa, idan zaku yi mu'amalar bashi, wato sashenku zai ba sashe bashi zuwa wani lokaci iyakantacce, to ku rubuta wannan bashi. A samu mai rubutu adali a cikinku, ya rubuta bashin bisa adalci da abin da ya dace da shari'a. kada wannan marubuci ya qi rubuta bashin a kan abin da Allah ya sanar da shi, na yin rubutu da adalci, ya rubuta abin da wanda ake bi bashin ya yi masa shiftar shi (wato ya faxa masa) don hakan ya zama tabbatarwa ne daga wajensa, amma ya ji tsoron Allah Ubangijinsa, kada ya rage komai daga cikinsa, ta vangaren gwargwadon abin ne, ko kalarsa ko yadda yake. Idan wanda ake bi bashin baya iya sarrafa abubuwa, ko yana da rauni saboda qanqanta, ko hauka, ko ba zai iya shifta ba (wato ba zai iya faxar abin da ake bin sa ba) saboda baya magana, to waliyyinsa wanda yake kula da shi ya yi shifta a madadinsa a bisa adalci. Ku nemi shaidar mutum biyu masu hankali adalai, idan ba a samu maza biyu ba, to a nemi shaidar namiji xaya da mata biyu, waxanda kuka yarda da addininsu da amanarsu, don idan xaya daga cikinsu ta manta, sai xayar ta tina mata. Kada masu shaida su qi yin shaida a kan bashi idan an neme su, wajibi ne a kansu su ba da shaida idan an kira su, kada qosawa ta same ku, wajen rubuta bashi, kaxan ne ko da yawa zuwa lokacin da aka iyakance. Rubuta bashi shi ne mafi daidai a shari'ar Allah, kuma shi ya fi kai wa matuqa wajen tsayar da shaida da bada ita, kuma ya fi kusa da kore shakka a cikin nau'in bashi da gwargwadonsa da lokacinsa, sai dai idan abin da kuka qulla kasuwanci ne a tsakaninku, na haja da kuxi hannu ne, to a lokacin babu laifi a kanku idan ba a rubuta ba, saboda ba buqatar hakan. An shar'anta muku shaida ne don yanke sababan savani a tsakaninku. Baya halatta a cutar da masu rubutu da shaidu, su ma ba ya hallata gare su, su cutar da wanda ya nemi rubutunsu ko shaidarsu. Idan aka samu cutarwa daga gareku, to hakan fita ne daga xa'ar Allah zuwa savonsa. Ku ji tsoron Allah – Ya ku muminai – ta hanyar ku kamanta abin da aka umarce ku, ku nisanci abin da aka hana ku. Allah yana sanar da ku abin da yake a cikinsa akwai gyaruwar duniyarku da lahirarku. Allah masani ne da dukkan komai, babu abin da yake vuya daga gare shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Halaccin tabbatar da bashi da sauran mu'amalolin dukiya, saboda kawar da savani da jayayya.**

**2 - Wajabcin ambaton lokacin biya a dukkan al'amuran bashi da qwadago.**

**3 - Tabbatar da walicci ga waxanda suke qanana, saboda gazawarsu, ko raunin hankalinsu, ko qanqantar shekarunsu.**

**4 - Shar'ancin kafa shaida wajen tabbatar da bashi da sauran haqqoqi.**

**5 - Yana daga cikin cikar rubutu da adalci, Marubuci ya kyautata rubutu da bayani da amfani da lafuzza waxanda aka amince da su, kowace mu'amala da gwargwadonta.**

**6 - Ba ya halatta a cutar da wani saboda tabbatar da bashi da rubuta shi, ta vangaren masu haqqi ne, ko ta vangaren wanda yake rubutawa, kuma ya yi shaida a kai.**

ثلاثة أرباع الحزب ٥

۞ وَإِن كُنتُمْ عَلَىٰ سَفَرٍ وَلَمْ تَجِدُوا۟ كَاتِبًا فَرِهَٰنٌ مَّقْبُوضَةٌ ۖ
فَإِنْ أَمِنَ بَعْضُكُم بَعْضًا فَلْيُؤَدِّ ٱلَّذِى ٱؤْتُمِنَ أَمَٰنَتَهُۥ وَلْيَتَّقِ
ٱللَّهَ رَبَّهُۥ ۗ وَلَا تَكْتُمُوا۟ ٱلشَّهَٰدَةَ ۚ وَمَن يَكْتُمْهَا فَإِنَّهُۥٓ
ءَاثِمٌ قَلْبُهُۥ ۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ عَلِيمٌ ﴿٢٨٣﴾ لِّلَّهِ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۗ وَإِن تُبْدُوا۟ مَا فِىٓ أَنفُسِكُمْ أَوْ تُخْفُوهُ
يُحَاسِبْكُم بِهِ ٱللَّهُ ۖ فَيَغْفِرُ لِمَن يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ ۗ
وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢٨٤﴾ ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيْهِ
مِن رَّبِّهِۦ وَٱلْمُؤْمِنُونَ ۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ
وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ مِّن رُّسُلِهِۦ ۚ وَقَالُوا۟
سَمِعْنَا وَأَطَعْنَا ۖ غُفْرَانَكَ رَبَّنَا وَإِلَيْكَ ٱلْمَصِيرُ ﴿٢٨٥﴾ لَا يُكَلِّفُ
ٱللَّهُ نَفْسًا إِلَّا وُسْعَهَا ۚ لَهَا مَا كَسَبَتْ وَعَلَيْهَا مَا ٱكْتَسَبَتْ ۗ
رَبَّنَا لَا تُؤَاخِذْنَآ إِن نَّسِينَآ أَوْ أَخْطَأْنَا ۚ رَبَّنَا وَلَا تَحْمِلْ
عَلَيْنَآ إِصْرًا كَمَا حَمَلْتَهُۥ عَلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِنَا ۚ رَبَّنَا
وَلَا تُحَمِّلْنَا مَا لَا طَاقَةَ لَنَا بِهِۦ ۖ وَٱعْفُ عَنَّا وَٱغْفِرْ لَنَا
وَٱرْحَمْنَآ ۚ أَنتَ مَوْلَىٰنَا فَٱنصُرْنَا عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٨٦﴾



**(283) Idan kun kasance matafiya, ba ku samu wanda zai rubuta muku takardar bashi ba, to ya isar a ba wanda zai ba da bashin ( wato mai haqqi) jingina, wadda zai karva daga wanda yake bi bashi, don ta zama lamuni a kan haqqinsa, har zuwa lokacin da wanda ake bi bashi, zai biya abin da yake kanshi na bashi. Idan sashe ya aminta da sashe a kan ba lallai ba ne a samu rubutu da shaidu da jingina ba, to sai bashin ya zama amana ne a wuyan wanda ake bi a wannan lokaci, kuma wajibi ne a kansa ya biya wanda yake bin shi, kamar yadda yake wajibi ne a kanshi ya ji tsoron Allah a cikin wannan amana, kada ya yi musun komai a cikinta. Idan ya yi musu, to wanda ya halarci mu'amalar ya ba da shaida, baya halatta ya voye shaidarsa a wannan lokaci. Duk wanda ya voye ta, to zuciyarsa, zuciyar fajiri ce. Allah ya san abin da kuke aikatawa, babu wani abin da yake voyuwa a gare shi, kuma zai saka muku a kan ayyukanku.**

**(284) Na Allah ne kaxai abin da yake cikin sammai da qassai, halittarsa ne, mulkinsa ne, tsarinsa ne. Idan kuka bayyana abin da yake cikin zukatanku ko kuka voye shi, Allah ya san shi, kuma zai muku hisabi a kanshi. Ya gafartawa wanda ya ga dama bayan haka, saboda falalarsa da rahama. Ya azabta wanda ya ga dama, bisa adalci da hikima. Allah mai iko ne a kan dukkan komai.**

**(285) Manzo Muhammad (S.A.W) ya yi imani da duk abin da aka saukar masa daga Ubangijinsa, haka ma muminai su ma sun yi imani, dukkaninsu sun yi imani da Allah, sun yi imani da dukkan Mala'ikunsa, da dukkan littattafansa da ya saukar da su ga Annabawa, da dukkan Manzanninsa waxanda ya aiko su, sun yi imani da su, kuma suka ce: "Ba zamu bambanta tsakanin wani daga Manzannin Allah ba". Sannan suka ce,: "Mun ji abin da ka umarce mu da shi, mun hanu daga abin da ka hana mu, mun bi ka da aikata abin da ka umarta, da barin abin da ka hana, muna roqonka ka gafarta mana ya Ubangijinmu, gareka makomarmu take kai kaxai, a cikin dukkan sha'aninmu.**

**(286) Allah ba ya xora wa wata rai sai abin da zata iya na daga ayyuka, saboda addinin Allah an gina shi ne a kan sauqi, babu wahala a cikinsa. Duk wanda ya aikata alheri, to yana da ladan abin da ya aikata, ba za a rage masa komai daga ciki ba. Wanda duk ya aikata sharri, to sakamakonsa na abin da ya aikata na zunubi yana kansa, ba wanda zai xauke masa. Manzo da Muminai suka ce: "Ya ubangijinmu kada ka yi mana uquba idan mun manta, ko mun yi kuskure a cikin aiki ko magana, ba da niyya ba. Ya Ubangijinmu kada ka xora mana abin da zai mana wahala, wanda ba za mu iya ba, kamar yadda ka xora wa waxanda suke gabaninmu, daga waxanda ka yi musu uquba saboda zalincinsu, kamar Yahudawa. Kada ka xora mana abin da zai mana wahala, wanda ba za mu iya ba, daga abubuwan da ka umarta a yi, da waxanda ka hana, Ka yafe mana zunubanmu, Ka gafarta mana. Ka jiqanmu da falalarka. Kai ne Majivincinmu, mai taimakonmu, ka taimake mu a kan mutane Kafirai.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Halaccin karvar jingina saboda samun lamunin biyan haqqi a yayin da aka rasa abin da za tabbatar da bashi da shi, sai dai idan masu mu'amalar, sashensu ya yarda da sashe.**

**2 - Cikar ilimin Allah Maxaukakin Sarki, da tsinkayar shi ga bayinsa, da cikakken ikonsa a kan yi musu hisabi a kan abin da suka aikata na ayyuka.**

**3 - A cikin wannan aya akwai tabbatar da rukunan imani da bayanin tushensa.**

**4 - Wannan addini ya ginu a kan sauqi da xauke wahala daga bayi. Allah baya xora musu komai, sai abin da za su iya, ba zai musu hisabi a kan abin da ba zasu iya ba.**

# SURATU ALI-IMRAN

-An Saukar Da Ita A Madinah –

سُورَةُ آلِ عِمۡرَانَ ٥٠ الجُزۡءُ الثَّالِثُ

سُورَةُ آلِ عِمۡرَانَ — آياتها ٢٠٠ — ترتيبها ٣

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓ ١ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡحَيُّ ٱلۡقَيُّومُ ٢ نَزَّلَ عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ
بِٱلۡحَقِّ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيۡهِ وَأَنزَلَ ٱلتَّوۡرَىٰةَ وَٱلۡإِنجِيلَ ٣ مِن
قَبۡلُ هُدٗى لِّلنَّاسِ وَأَنزَلَ ٱلۡفُرۡقَانَۗ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ
لَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدٞۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٞ ذُو ٱنتِقَامٍ ٤ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَخۡفَىٰ
عَلَيۡهِ شَيۡءٞ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فِي ٱلسَّمَآءِ ٥ هُوَ ٱلَّذِي يُصَوِّرُكُمۡ
فِي ٱلۡأَرۡحَامِ كَيۡفَ يَشَآءُۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٦ هُوَ
ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ مِنۡهُ ءَايَٰتٞ مُّحۡكَمَٰتٌ هُنَّ أُمُّ
ٱلۡكِتَٰبِ وَأُخَرُ مُتَشَٰبِهَٰتٞۖ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِمۡ زَيۡغٞ فَيَتَّبِعُونَ
مَا تَشَٰبَهَ مِنۡهُ ٱبۡتِغَآءَ ٱلۡفِتۡنَةِ وَٱبۡتِغَآءَ تَأۡوِيلِهِۦۖ وَمَا يَعۡلَمُ تَأۡوِيلَهُۥٓ
إِلَّا ٱللَّهُۗ وَٱلرَّٰسِخُونَ فِي ٱلۡعِلۡمِ يَقُولُونَ ءَامَنَّا بِهِۦ كُلّٞ مِّنۡ عِندِ
رَبِّنَاۗ وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّآ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٧ رَبَّنَا لَا تُزِغۡ قُلُوبَنَا بَعۡدَ
إِذۡ هَدَيۡتَنَا وَهَبۡ لَنَا مِن لَّدُنكَ رَحۡمَةًۚ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡوَهَّابُ ٨ رَبَّنَآ
إِنَّكَ جَامِعُ ٱلنَّاسِ لِيَوۡمٖ لَّا رَيۡبَ فِيهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُخۡلِفُ ٱلۡمِيعَادَ ٩

Suratu Ali-Imran 50 Juzu'ii 3

**Daga Manufofin Surar:** Tana bayani a kan tabbata a kan musulunci bayan Allah ya cika shi, kuma ya bayyana shi, sannan tana raddi ga shubuhohin ma'abota littafi, musamman ma Nasara.

**Tafsiri:** Wannan sura ce da aka saukar a Madinah, an kira ta da sunan Ali-Imran ne saboda ambaton Ali-Imran da ya zo a aya ta (33) a cikin surar.

(1) Alif, Laam, Meem. Waxannan xaixaikun haruffa irinsu sun gabata a farkon suratul Baqara, kuma su nuni ne zuwa ga gazawar larabawa wajen zuwa da irin wannan Alqur'ani, wanda aka haxa shi da irin waxannan haruffa, waxanda aka buxe surar da su, ga shi kuma da su ne suke maganganunsu ba wasu ba ne daban. (2) Allah wanda babu abin bautawa da cancanta da gaskiya sai Shi, Shi kaxai ba waninsa ba. Rayayye, cikakkiyar rayuwa, wadda ba mutuwa ba tawaya a cikinta. Tsayayyen da ya tsaya da kansa, ya wadatu daga dukkan halitta, kuma da shi dukkan halitta suka tsaya, ba za su iya wadatuwa daga gare shi ba a kowane hali da yanayi ba.

(3) (4) Ya saukar maka da Alqur'ani – Ya kai wannan Annabi – wanda labaran cikinsa gaskiya ne, hukunce-hukuncensa kuma adalci ne, sannan ya dace da littafan Allah waxanda suka gabace shi, babu karo a tsakaninsu. Ya saukar da Attaura ga Annabi Musa, Injila kuma ga Annabi Isa (A.S) tun gabanin saukar maka da Alqur'ani. Waxannan littatafan da Allah ya saukar dukkaninsu shiriya ne da faxakarwa ga mutane, kuma suna kira zuwa ga abin da yake gyaruwar addininsu ne da rayuwarsu. Allah ya saukar da Alfurqan wanda da shi ake sanin gaskiya da varna, shiriya da vata. Waxanda suka kafircewa ayoyin Allah, waxanda ya saukar maka suna da azaba mai tsanani. Allah Mabuwayi ne babu abin da yake rinjayarsa, Ma'abocin kamu ne ga wanda ya qaryata Manzanninsa, ya savawa umarninsa. (5) Haqiqa Allah babu abin da yake vuya gare shi a cikin qasa da sama, iliminsa ya kewaye da dukkan komai, na fili da na voye. (6) Shi ne wanda ya halicceku da kamanni daban daban, daga cikin iyayenku, kuma a kan yadda ya ga dama, namiji ko mace, mai kyau ko mummuna, fari ko baqi. Babu wani abin bautawa da cancanta wanda ba shi ba. Mabuwayi da ba a rinjaye a kansa. Mai hikima a cikin halittarsa da tsarinsa da shari'arsa. (7) Shi ne wanda ya saukar maka da Alqur'ani – Ya kai wannan Annabi – a cikinsa akwai ayoyin da ma'anarsu a fili take, babu wani duhu a cikinsu, su ne tushe kuma mafi yawancin Alqur'ani, kuma su ne makoma yayin savani. Sannan cikinsa akwai ayoyin da suke xaukar ma'ana fiye da xaya, wato ma'anarsu tana shiga duhu a wurin da yawa daga cikin mutane. Waxanda a cikin zuciyarsu akwai karkacewa gaskiya, sai su bar ayoyin da suke bayyanannu, su xauki waxanda suke da ma'ana fiye da xaya, don tayar da shubuha ga mutane da vatar da su, sannan kuma suna fassara su da son zuciyarsu, da abin da ya dace da hanyar da suke kai vatacciya. Ba wanda ya san haqiqanin ma'anar waxannan ayoyi da qarshen abin da suke nunawa sai Allah. Malamai masu zurfin ilimi suna cewa: Mun yi imani da Alqur'ani gaba xaya, saboda dukkaninsa daga Ubangijinmu yake, suna fassara ayoyin da suke xauke da ma'ana fiye da xaya da ayoyin da suke bayyanannu. Ba kowa yake wa'azantuwa ba sai masu lafiyayyen hankali. (8) Waxannan malaman masu zurfin ilimi, suna cewa: "Ya Ubangijinmu kada ka karkatar da zukatanmu daga gaskiya bayan ka shiryar da mu, ka kuvutar damu daga abin da ya samu karkatattu, waxanda suka kaucewa gaskiya. Ka bamu rahama mai yalwa daga wurinka, ka shiryar da zukatanmu da ita, ka kare mu daga vata. Haqiqa Kai – Ya Ubangijinmu –kai ne mai horewa mai yawan kyauta. (9) Ya Ubangijinmu haqiqa zaka tara mutane gaba xaya don yi musu hisabi, a ranar da ba shakka a cikinta, wadda take zuwa ba makawa. Haqiqa – Ya Ubangijinmu – ba ka sava alqawari.

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Allah ya tsayar da hujja, ya yanke uzuri ga halitta da aiko da Manzanni, da saukar da littattafai, waxanda suke shiryar wa zuwa ga gaskiya, suna tsoratarwa daga varna. 2 - Cikar ilimin Allah da kewayewarsa ga halitta. Babu abin da yake vuya daga gare shi a cikin qasa ko sama, a fili yake ko a voye. 3 - Daga abin da muminai da malamai masu ilimi suke kai fassara ayoyin da ma'anoninsu suke da rikitarwa a kan hasken ayoyin da suke bayyanannu. 4 - Shar'ancin addu'a da roqon Allah a kan tabbata a kan gaskiya, da shiriya a cikin kowane lamari, musamman ma a lokacin fitinu da son zuciya.

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَن تُغۡنِيَ عَنۡهُمۡ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُم
مِّنَ ٱللَّهِ شَيۡـٔٗاۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ وَقُودُ ٱلنَّارِ ١٠ كَدَأۡبِ ءَالِ
فِرۡعَوۡنَ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ
بِذُنُوبِهِمۡۗ وَٱللَّهُ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ١١ قُل لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ
سَتُغۡلَبُونَ وَتُحۡشَرُونَ إِلَىٰ جَهَنَّمَۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ١٢
قَدۡ كَانَ لَكُمۡ ءَايَةٞ فِي فِئَتَيۡنِ ٱلۡتَقَتَاۖ فِئَةٞ تُقَٰتِلُ فِي
سَبِيلِ ٱللَّهِ وَأُخۡرَىٰ كَافِرَةٞ يَرَوۡنَهُم مِّثۡلَيۡهِمۡ رَأۡيَ
ٱلۡعَيۡنِۚ وَٱللَّهُ يُؤَيِّدُ بِنَصۡرِهِۦ مَن يَشَآءُۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَعِبۡرَةٗ لِّأُوْلِي ٱلۡأَبۡصَٰرِ ١٣ زُيِّنَ لِلنَّاسِ حُبُّ ٱلشَّهَوَٰتِ
مِنَ ٱلنِّسَآءِ وَٱلۡبَنِينَ وَٱلۡقَنَٰطِيرِ ٱلۡمُقَنطَرَةِ مِنَ ٱلذَّهَبِ
وَٱلۡفِضَّةِ وَٱلۡخَيۡلِ ٱلۡمُسَوَّمَةِ وَٱلۡأَنۡعَٰمِ وَٱلۡحَرۡثِۗ ذَٰلِكَ
مَتَٰعُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَٱللَّهُ عِندَهُۥ حُسۡنُ ٱلۡمَـَٔابِ ١٤ ۞ قُلۡ الحزب ٦
أَؤُنَبِّئُكُم بِخَيۡرٖ مِّن ذَٰلِكُمۡۖ لِلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ عِندَ رَبِّهِمۡ
جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَأَزۡوَٰجٞ
مُّطَهَّرَةٞ وَرِضۡوَٰنٞ مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِٱلۡعِبَادِ ١٥



**(10) Waxanda suka kafirce wa Allah da Manzanninsa dukiyoyinsu da 'ya'yansu ba za su kare su daga azabar Allah ba, a duniya ko a lahira. Waxanda suka siffatu da waxannan siffofin su ne qiraren wutar Jahannama, waxanda ake rurutata da su a ranar alqiyama.**

**(11) Sha'anin waxannan kafirai kamar sha'anin mabiya Fir'auna ne da waxanda suke gabaninsu, daga cikin waxanda suka kafirce wa Allah, suka qaryata da ayoyinsa, sai Allah ya azabtar da su saboda zunubansu, don haka dukiyoyinsu da 'ya'yansu ba za su amfane su ba. Allah mai tsananin uquba ne ga wanda ya kafirce da shi, ya qaryata ayoyinsa.**

**(12) Ka ce wa dukkan waxanda suka kafirta – Ya kai Wannan Manzo -: Muminai za su ci galaba a kanku, kuma zaku mutu a kan kafirci, Allah ya tara ku a wutar Jahannama. Tir da wannan shimfixar ta ku.**

**(13) Kuna da dalilai da izina da zaku xauka daga qungiyoyi guda biyu, da suka haxu don yaqi a tsakaninsu a ranar Badar, xaya qungiyar muminai ne, ita ce ta Manzon Allah (S.A.W) da Sahabbansa, tana yaqi ne a kan tafarkin Allah, don kalmar Allah ta zama a sama, kalmar kafirai kuma a can qasa. Xayar qungiyar kuma kafirai ne, sune kafiran Makkah, waxanda suka fito cikin alfahari da riya da qabilanci. Muminai suna ganinsu a zahiri sun ninka su biyu, sai Allah ya taimaki waliyyansa, ya qarfafa wanda ya ga dama da nasararsa. A cikin wannan akwai izina da wa'azi ga waxanda suke da basira, saboda za su gane cewa nasara tana ga masu imani, koda kuwa su kaxan ne. Faxuwa da karyewa tana ga masu varna, koda kuwa suna da yawa.**

**(14) Allah yana ba da labari cewa ya jarrabi mutane, ya qawata musu abubuwan sha'awa na duniya, kamar mata, da 'ya'ya, da dukiya mai yawa, wadda ta haxa zinare da azurfa, da horarrun dawakai masu kyau, da dabbobin ni'ima, na daga Raquma, da Shanu, da Tumaki da Awaki, da shuka a bayan qasa. Duk waxannan jin daxin rayuwar duniya ne, ana jin daxi da su, wani lokaci xan kaxan, sai kuma su gushe, don bai dace ga mumini ya damu da su ba. A wajen Allah ne kaxai kyakkyawar makoma take, ita ce Aljannah, wadda faxinta, faxin sammai da qassai ne. Kasancewar abubuwan sha'awa na duniya suna yankewa, Sai Allah ya faxakar damu zuwa ga abin da ya fi alheri daga gare su, Ya ce:**

**(15) Ka ce – Ya kai wannan Manzo – In baku labarin abin da ya fi waxannan abubuwan sha'awar alheri? Su ne, Waxanda suka ji tsoron Allah, ta hanyar yi masa xa'a, da barin savonsa, suna da Aljannatai waxanda qoramu suke gudana a qarqashin gine-ginensu, da bishiyoyinsu, za su dauwama a cikinsu, ba mutuwa ko qarewa. Suna da mata masu tsarki daga dukkan wani abun qi, a halitta ko a halaye. Sannan duk da haka suna da yarda daga Allah, ba zai yi fushi da su ba, har abada. Allah yana kallon halayen bayi, babu wani abin da yake vuya a gare shi, kuma zai saka musu a kansu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Ruxuwar da kafirai suke yi da dukiyoyinsu da 'ya'yansu, ba zai wadatar musu da komai ba ranar alqiyama, kuma ba zai kare su daga azabar Allah idan ta sauka a kansu ba.**

**2 - Tabbas nasara ba ta ta'allaqa da yawa ko danadi ba, ta rataya ne da qarfafawar Allah da taimakonsa.**

**3 - Allah ya qawata wa mutane abubuwa kala-kala daga abubuwan sha'awar duniya don ya jarrabe su, kuma ya san waxanda za su tsaya a kan iyakokinsa da waxanda za su qetare su.**

**4 - Dukkan ni'imar duniya da jin daxinta kaxan ne, kuma za su gushe, ba kuma za a qiyasta su da abin da yake lahira, na ni'ima mai girma wadda ba ta gushe wa ba.**

ٱلَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَآ إِنَّنَآ ءَامَنَّا فَٱغۡفِرۡ لَنَا ذُنُوبَنَا
وَقِنَا عَذَابَ ٱلنَّارِ ١٦ ٱلصَّٰبِرِينَ وَٱلصَّٰدِقِينَ وَٱلۡقَٰنِتِينَ
وَٱلۡمُنفِقِينَ وَٱلۡمُسۡتَغۡفِرِينَ بِٱلۡأَسۡحَارِ ١٧ شَهِدَ ٱللَّهُ
أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَأُوْلُواْ ٱلۡعِلۡمِ قَآئِمَۢا
بِٱلۡقِسۡطِۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١٨ إِنَّ ٱلدِّينَ
عِندَ ٱللَّهِ ٱلۡإِسۡلَٰمُۗ وَمَا ٱخۡتَلَفَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ
إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡعِلۡمُ بَغۡيَۢا بَيۡنَهُمۡۗ وَمَن يَكۡفُرۡ
بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ١٩ فَإِنۡ حَآجُّوكَ
فَقُلۡ أَسۡلَمۡتُ وَجۡهِيَ لِلَّهِ وَمَنِ ٱتَّبَعَنِۗ وَقُل لِّلَّذِينَ أُوتُواْ
ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡأُمِّيِّـۧنَ ءَأَسۡلَمۡتُمۡۚ فَإِنۡ أَسۡلَمُواْ فَقَدِ ٱهۡتَدَواْۖ
وَّإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنَّمَا عَلَيۡكَ ٱلۡبَلَٰغُۗ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِٱلۡعِبَادِ ٢٠
إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكۡفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَيَقۡتُلُونَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ
بِغَيۡرِ حَقّٖ وَيَقۡتُلُونَ ٱلَّذِينَ يَأۡمُرُونَ بِٱلۡقِسۡطِ مِنَ
ٱلنَّاسِ فَبَشِّرۡهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ٢١ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ حَبِطَتۡ
أَعۡمَٰلُهُمۡ فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ٢٢



**(16) 'Yan Aljannah su ne waxanda suke cewa a cikin addu'arsu: Ya Ubangijinmu, haqiqa mun yi imani da kai, da abin da ka saukar ga Manzanninka, mun bi shari'arka, ka gafarta mana abin da muka yi na zunubai, ka nisantar damu daga azabar wuta.**

**(17) Su ne masu haquri a wajen aikata ayyukan xa'a, da barin munanan ayyuka, da abin da ya same su na bala'i. su ne masu gaskiya a cikin maganganunsu da ayyukansu. Su ne masu yi wa Allah cikakkiyar biyayya. Su ne masu ciyar da dukiyoyinsu saboda Allah. Su ne masu neman gafara a qarshen dare, saboda addu'ar a wannan lokaci ta fi kusa da amsawa, kuma zuciya tana wofinta daga abubuwan shagala.**

**(18) Allah ya shaida kan cewa shi ne abin bauta da gaskiya ba waninsa ba, saboda abin da ya tsayar na ayoyin da ake karantawa (Wato Al-ayatush Shar'iyyah) da waxanda ake gani (Wato Al-Kauniyyah) waxanda suke nuna cancantar shi da bauta. Mala'iku ma sun shaida da haka. Malamai ma sun shaida da haka, ta hanyar bayanin kaxaita shi da suke yi, da kira zuwa gare shi. Sai suka shaida da mafi girman abin da ake shaidawa, shi ne kaxaita Allah (Wato Tauhidi) da tsayuwarsa da adalci a cikin halittarsa da shari'arsa. Babu abin bautawa da gaskiya sai Shi, Mabuwayi wanda babu mai rinjayarsa, Mai hikima a cikin halittarsa da tsarinsa, da shari'arsa.**

**(19) Haqiqanin addini karvavve a wurin Allah shi ne Musulunci. Shi ne jayuwa ga Allah shi kaxai, da yi masa xa'a, da miqa wuya da bauta gare shi, da imani da Manzanni gaba xaya, har zuwa cikamakinsu Annabi Muhammad (S.A.W), wanda Allah ya cika manzanci da shi, ba zai karvi wata shari'a wadda ba ta shi ba. Yahudawa da Nasara basu yi savani a cikin addininsu ba, ba su rabu qungiya – qungiya, jama'a jama'a ba, sai bayan da hujja ta tsaya a kansu, ilimi ya zo musu, saboda hassada da kwaxayin duniya. Duk wanda ya kafirce wa ayoyin Allah, waxanda ya saukar ga Manzonsa, to haqiqa Allah mai gaggawar hisabi ne ga wanda ya kafirce masa, ya qaryata Manzanninsa.**

**(20) Idan suka yi jayayya da kai – Ya kai Wannan Manzo – a cikin gaskiyar da ta sauka a gare ka, to ka amsa musu ka ce,: "Ni da waxanda suka bi ni, daga cikin muminai mun miqa wuya ga Allah Maxaukakin Sarki". Ya kai wannan Manzo ka tambayi ma'abota littafi da mushirikai ka ce musu: "kun miqa wuya ga Allah, kuna masu tsarkake zuciyarku gare shi, masu bin abin da na zo da shi?". Idan sun miqa wuya ga Allah, sun bi shari'arka, to sun kama hanyar shiriya, idan kuwa suka bijire daga musulunci, to babu abin da yake kanka sai dai ka isar musu da abin da aka aiko ka da shi, lamarinsu yana ga Allah, Shi Maxaukakin Sarki yana ganin bayinsa, kuma zai saka wa dukkan wani mai aiki da abin da ya aikata.**

**(21) Waxanda suka kafirce wa hujjojin Allah waxanda ya saukar musu, suke kashe Annabawa ba da haqqi ba, sai kawai don zalunci da qetare iyaka, suke kashe waxanda suke umarni da adalci daga cikin mutane, waxanda suke umarni da kyakkyawan aiki, suke hana mummunan aiki. To kafirai masu wannan aiki ka yi musu bushara da azaba mai raxaxi.**

**(22) Waxanda suka siffatu da waxannan siffofi, ayyukansu sun rushe, ba su amfanu da su ba a duniya ko a lahira, saboda ba su yi imani da Allah ba, kuma ba su da mataimaka da za su kare su daga azaba.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Daga mafi girman abin da yake kankare zunubai, ya kare mutum daga azabar wuta, imani da Allah Maxaukakin Sarki, da bin abin da Manzo (S.A.W) ya zo da shi. 2 - Mafi girman shaida ita ce, shaidawar cancantar Allah Maxaukakin Sarki da bauta, don haka Allah ya yi wa kansa shaida da ita, Mala'iku ma suka shaida da ita, hakama masu ilimi daga halitta su ma sun shaida. 3 - Zalunci da hassada suna daga cikin mafi girman abubuwan da suke kawo savani da kaucewa gaskiya.**

أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ أُوتُواْ نَصِيبٗا مِّنَ ٱلۡكِتَٰبِ يُدۡعَوۡنَ إِلَىٰ كِتَٰبِ
ٱللَّهِ لِيَحۡكُمَ بَيۡنَهُمۡ ثُمَّ يَتَوَلَّىٰ فَرِيقٞ مِّنۡهُمۡ وَهُم مُّعۡرِضُونَ ٢٣
ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَالُواْ لَن تَمَسَّنَا ٱلنَّارُ إِلَّآ أَيَّامٗا مَّعۡدُودَٰتٖۖ
وَغَرَّهُمۡ فِي دِينِهِم مَّا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ ٢٤ فَكَيۡفَ إِذَا جَمَعۡنَٰهُمۡ
لِيَوۡمٖ لَّا رَيۡبَ فِيهِ وَوُفِّيَتۡ كُلُّ نَفۡسٖ مَّا كَسَبَتۡ وَهُمۡ
لَا يُظۡلَمُونَ ٢٥ قُلِ ٱللَّهُمَّ مَٰلِكَ ٱلۡمُلۡكِ تُؤۡتِي ٱلۡمُلۡكَ مَن
تَشَآءُ وَتَنزِعُ ٱلۡمُلۡكَ مِمَّن تَشَآءُ وَتُعِزُّ مَن تَشَآءُ وَتُذِلُّ مَن
تَشَآءُۖ بِيَدِكَ ٱلۡخَيۡرُۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٦ تُولِجُ ٱلَّيۡلَ
فِي ٱلنَّهَارِ وَتُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِي ٱلَّيۡلِۖ وَتُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ
وَتُخۡرِجُ ٱلۡمَيِّتَ مِنَ ٱلۡحَيِّۖ وَتَرۡزُقُ مَن تَشَآءُ بِغَيۡرِ حِسَابٖ ٢٧
لَّا يَتَّخِذِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلۡكَٰفِرِينَ أَوۡلِيَآءَ مِن دُونِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۖ
وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ فَلَيۡسَ مِنَ ٱللَّهِ فِي شَيۡءٍ إِلَّآ أَن تَتَّقُواْ مِنۡهُمۡ
تُقَىٰةٗۗ وَيُحَذِّرُكُمُ ٱللَّهُ نَفۡسَهُۥۗ وَإِلَى ٱللَّهِ ٱلۡمَصِيرُ ٢٨ قُلۡ
إِن تُخۡفُواْ مَا فِي صُدُورِكُمۡ أَوۡ تُبۡدُوهُ يَعۡلَمۡهُ ٱللَّهُۗ وَيَعۡلَمُ
مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٩



**(23) Ya kai wannan Annabi baka ga halin Yahudawa ba, waxanda Allah ya basu wani rabo na ilimin Attaura da abin da ta nuna na annabcinka, ana kiransu zuwa ga komawa littafin Allah Attaura, don ya zama alkali agare su, cikin abin da suka yi savani a kansa, amma sai wasu vangare daga cikin malamansu da shugabanninsu suka juya baya, suka bijirewa hukuncin littafin, saboda bai dace da son zuciyarsu ba. Alhali abin da yafi dacewa da su – tunda suna riya cewa suna bin littafin – su zama waxanda za su riga dukkan mutane zuwa hukunci da shi.**

**(24) Sun yi wannan juyawa da bijirewa ga barin gaskiya ne saboda suna da'awar cewa wuta ba zata shafe su ba a ranar alqiyama sai 'yan kwanaki kaxan, sannan su shiga Aljannah. Wannan zaton da suka qirqiro na qarya da varna, shi ya sa suka yi tsaurin ido a kan Allah da addininsa.**

**(25) Yaya halinsu da nadamarsu za su kasance?. Haqiqa za su kasance a cikin tsananin muni, idan muka tara su don yin hisabi a ranar da ba shakka a cikinta, ita ce ranar alqiyama. Aka ba wa kowace rai sakamakon abin da ta aikata, kamar yadda ya cancanta da ita, ba tare da zalunci ba, ta hanyar rage wa wata rai ladan kyawawan ayyukanta, ko yi mata qari a cikin sakamakon munanan ayyukanta ba.**

**(26) Ka ce – Ya kai wannan Manzo – kana mai yabo da girmama Allah -: Ya Allah kai ne mamallakin mulki gaba xaya, a duniya da lahira, kana ba wanda ka ga dama mulki daga cikin halittarka, kana kuma fizge shi daga wanda ka ga dama, kana xaukaka wanda ka ga dama, kana qasqanta wanda ka ga dama. Kana aikata dukkan wannan cikin hikima da adalci. A hannunka kai kaxai dukkan alheri yake, kuma Kai mai iko ne a kan dukkan komai.**

**(27) Daga abin da yake nuna ikonka ya Allah, kana shigar da dare cikin yini, sai yinin ya yi tsawo, kana shigar da yini a cikin dare, sai daren ya yi tsawo, kana fitar da mai rai daga matacce, kamar fitar da mumini daga kafiri, shuka daga qwaya. Kana fitar matacce daga mai rai, kamar kafiri daga mumini, qwai daga kaza. Kana azurta wanda ka ga dama arziki mai yalwa, ba tare da wani lissafi ko qirgawa ba.**

**(28) Ya ku Muminai kada ku riqi kafirai masoya, kuna son su, kuna taimakonsu, ku bar muminai. Duk wanda ya aikata haka to ya barranta daga Allah, Allah ma ya barranta daga gare shi, sai dai idan kuna cikin ikonsu, kuna jin tsoronsu, to babu laifi ku kiyayi cutarwarsu, ta hanyar tausasawa a cikin zance, ko a aiki, amma tare da voye gabarku gare su. Allah yana tsoratar daku kansa, ku ji tsoronsa, kada ku yi abin da zai jawo fushinsa, ta hanyar yin zunubai. Wurin Allah kaxai bayi za su koma ranar alqiyama, don ya saka musu a kan ayyukansu.**

**(29) Ka ce da su – Ya kai wannan Annabi – idan kuka voye abin da yake cikin zukatanku, na daga abin da Allah ya hana ku, kamar jivinta da son kafirai, ko kuka bayyana haka, Allah ya san shi, babu wani abu da yake vuya daga gare shi, ya san abin da yake cikin sammai da qassai. Allah mai iko ne akan dukkan komai, babu wani abu da yake gagararsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa :

**1 - Dacewa da shiriya duk daga Allah ne. kuma komai yawan ilimi, koda mai shi ya kai qoluluwar martaba, idan bai haxu da dacewa daga Allah ba, to mai shi bai zai amfane shi ba.**

**2 - Mulki na Allah ne, shi yake bayarwa, shi yake hanawa, shi yake xaukakawa, kuma yake qasqantarwa. Dukkan alheri yana hannunsa, kuma gare shi ake mayar da dukkan al'amura, ba roqon wani wanda ba shi ba.**

**3 - Haxarin jivintar kafirai da son su, saboda irin alqawarin narkon azaba da Allah ya yi wa wanda ya aikata haka, na barranta daga gare shi, da kuma yi masa hisabi ranar alqiyama.**

يَوْمَ تَجِدُ كُلُّ نَفْسٍ مَّا عَمِلَتْ مِنْ خَيْرٍ مُّحْضَرًا وَمَا عَمِلَتْ
مِن سُوٓءٍ تَوَدُّ لَوْ أَنَّ بَيْنَهَا وَبَيْنَهُۥٓ أَمَدًۢا بَعِيدًا ۗ وَيُحَذِّرُكُمُ ٱللَّهُ
نَفْسَهُۥ ۗ وَٱللَّهُ رَءُوفٌۢ بِٱلْعِبَادِ ٣٠ قُلْ إِن كُنتُمْ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ
فَٱتَّبِعُونِى يُحْبِبْكُمُ ٱللَّهُ وَيَغْفِرْ لَكُمْ ذُنُوبَكُمْ ۗ وَٱللَّهُ غَفُورٌ
رَّحِيمٌ ٣١ قُلْ أَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ ۖ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ
ٱلْكَٰفِرِينَ ٣٢ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصْطَفَىٰٓ ءَادَمَ وَنُوحًا وَءَالَ إِبْرَٰهِيمَ الحزب ٦
وَءَالَ عِمْرَٰنَ عَلَى ٱلْعَٰلَمِينَ ٣٣ ذُرِّيَّةًۢ بَعْضُهَا مِنۢ بَعْضٍ ۗ وَٱللَّهُ
سَمِيعٌ عَلِيمٌ ٣٤ إِذْ قَالَتِ ٱمْرَأَتُ عِمْرَٰنَ رَبِّ إِنِّى نَذَرْتُ لَكَ
مَا فِى بَطْنِى مُحَرَّرًا فَتَقَبَّلْ مِنِّىٓ ۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ٣٥
فَلَمَّا وَضَعَتْهَا قَالَتْ رَبِّ إِنِّى وَضَعْتُهَآ أُنثَىٰ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا وَضَعَتْ
وَلَيْسَ ٱلذَّكَرُ كَٱلْأُنثَىٰ ۖ وَإِنِّى سَمَّيْتُهَا مَرْيَمَ وَإِنِّىٓ أُعِيذُهَا بِكَ
وَذُرِّيَّتَهَا مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ ٱلرَّجِيمِ ٣٦ فَتَقَبَّلَهَا رَبُّهَا بِقَبُولٍ
حَسَنٍ وَأَنۢبَتَهَا نَبَاتًا حَسَنًا وَكَفَّلَهَا زَكَرِيَّا ۖ كُلَّمَا دَخَلَ عَلَيْهَا
زَكَرِيَّا ٱلْمِحْرَابَ وَجَدَ عِندَهَا رِزْقًا ۖ قَالَ يَٰمَرْيَمُ أَنَّىٰ لَكِ هَٰذَا ۖ
قَالَتْ هُوَ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ يَرْزُقُ مَن يَشَآءُ بِغَيْرِ حِسَابٍ ٣٧



**(30) Ranar alqiyama kowace rai za ta ga dukkan ayyukanta na alheri an zo da su, babu abin da aka rage daga cikinsu. Wadda ta yi mummunan aiki za ta yi burin, ina ma tsakaninta da tsakanin waxannan ayyuka akwai zamani mai nisa, amma kuma ba za ta samu abin da tai buri ba. Allah yana tsoratar da ku kansa, kada ku yi abin zai sa ya yi fushi, ta hanyar yin savo. Allah mai jinqan bayinsa ne, don haka yake jan kunnensu, yake tsoratar da su.**

**(31) Ka ce – Ya kai wannan Manzo – in kuna son Allah da gaske, to ku bi abin da na zo da shi, a fili da voye, idan kuka aikata haka, sai ku samu son Allah, kuma ya gafarta muku zunubanku. Allah mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa, mai jinqan su ne.**

**(32) Ka ce – Ya kai wannan Manzo – ku bi Allah, ku bi Manzonsa, ta hanyar kamanta umarni, da nisantar abin da aka hana. Idan kuka bijirewa yin hakan, to ku sani Allah ba ya son kafirai, masu sava wa umarninsa da umarnin Manzonsa.**

**(33) Haqiqa Allah ya zavi Annabi Adam (A.S) ya sanya Mala'ikunsa suka yi masa sujjada. Ya zavi Annabi Nuhu, ya sanya shi farkon Manzo zuwa ga mutanen da suke bayan qasa. Ya zavi iyalan Annabi Ibrahim ya sanya Annabci ya wanzu a cikin zuriyarsa. Ya zavi iyalan Imrana. Dukkan waxannan ya zave su, ya fifita su a kan mutanen zamaninsu.**

**(34) Waxannan da aka ambata daga Annabawa da zurriyarsu, waxanda suka bi hanyarsu, to zuriya ce da sashenta daga sashe yake, a wajen kaxaita Allah da ayyuka nagari, suna gadon kyawawan halaye daga sashensu. Allah yana jin maganganun bayinsa, kuma ya san ayyukansu, don haka ya zavi waxanda ya ga dama daga cikinsu, ya fifita waxanda ya ga dama daga cikinsu.**

**(35) Ka tuna – Ya kai wannan Manzo – yayin da matar Imran, mahaifiyar Maryam (A.S) ta ce: "Ya Ubangiji ni na wajabtawa kaina, zan sanya abin da yake cikin cikina ya zama naka kai kaxai, na yanta shi daga dukkan wata hidima, don ya yi maka hidima, ya yi wa xakinka hidima, ka karva daga gare ni. Haqiqa Kai mai jin addu'ata ne, kuma masani ne ga niyyata.**

**(36) Da cikinta ya cika watannin haihuwa, ta haife abin da yake cikinta xin. Sai ta ce – tana mai ba da uzuri, domin tana zaton cikin nata namiji ne – ta ce: "Ya Ubangiji na haife ta mace" – Allah ya fi ta sanin abin da ta haifa – namijin da take fata ta samu ba kamar macen da aka ba ta yake ba, wajen qarfin halitta. Ta ci gaba da cewa: "Na sa mata suna Maryam, na kuma tsareta da tsarinka da zuriyarta daga Shaixan, wanda aka kore shi daga rahamarka.**

**(37) Sai Allah ya karvi bakancenta da kyakkyawan karva, ya tayar da ita kyakkyawar tayarwa, ya sanya zukatan mutanen qwarai daga cikin bayinsa suna tausayinta. Ya sanya renonta a hannun Annabi Zakariyya (A.S). Sai ya kasance koyaushe Annabi Zakariyya ya shiga wurinta, wurin da take ibada, sai ya samu arziki mai daxi a wurinta. Don haka sai ya yi mata magana ya ce mata: "Ya Maryam daga ina wannan arzikin yake?" Sai ta bashi amsa ta ce: "Wannan arzikin daga wajen Allah ne, haqiqa Allah yana azurta wanda ya ga dama, arziki mai yalwa, ba tare da lissafi ba".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Girman Allah da tsananin uqubarsa yakan sanya mai hankali ya kiyayi savawa umarninsa Maxaukakin Sarki.**

**2 - Dalilin da yake nuna son Allah na gaskiya da son Manzonsa, shi ne bin shari'a a wajen umarni da hani. Amma da'awar so babu biyayya, ba za ta amfani mai yin ta da komai ba.**

**3 - Allah yana zavar wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, ya ba su Annabci da ibada, da hikimarsa da rahamarsa. Zai ma iya kevance su da ayoyi, waxanda suka savawa al'ada.**

هُنَالِكَ دَعَا زَكَرِيَّا رَبَّهُۥ قَالَ رَبِّ هَبْ لِي مِن لَّدُنكَ ذُرِّيَّةً
طَيِّبَةً إِنَّكَ سَمِيعُ الدُّعَآءِ ٣٨ فَنَادَتْهُ الْمَلَٰٓئِكَةُ وَهُوَ قَآئِمٌ
يُصَلِّي فِي الْمِحْرَابِ أَنَّ اللَّهَ يُبَشِّرُكَ بِيَحْيَىٰ مُصَدِّقًا بِكَلِمَةٍ
مِّنَ اللَّهِ وَسَيِّدًا وَحَصُورًا وَنَبِيًّا مِّنَ الصَّٰلِحِينَ ٣٩ قَالَ رَبِّ
أَنَّىٰ يَكُونُ لِي غُلَٰمٌ وَقَدْ بَلَغَنِيَ الْكِبَرُ وَامْرَأَتِي عَاقِرٌ قَالَ
كَذَٰلِكَ اللَّهُ يَفْعَلُ مَا يَشَآءُ ٤٠ قَالَ رَبِّ اجْعَل لِّيٓ ءَايَةً
قَالَ ءَايَتُكَ أَلَّا تُكَلِّمَ النَّاسَ ثَلَٰثَةَ أَيَّامٍ إِلَّا رَمْزًا وَاذْكُر
رَّبَّكَ كَثِيرًا وَسَبِّحْ بِالْعَشِيِّ وَالْإِبْكَٰرِ ٤١ وَإِذْ قَالَتِ
الْمَلَٰٓئِكَةُ يَٰمَرْيَمُ إِنَّ اللَّهَ اصْطَفَىٰكِ وَطَهَّرَكِ وَاصْطَفَىٰكِ
عَلَىٰ نِسَآءِ الْعَٰلَمِينَ ٤٢ يَٰمَرْيَمُ اقْنُتِي لِرَبِّكِ وَاسْجُدِي
وَارْكَعِي مَعَ الرَّٰكِعِينَ ٤٣ ذَٰلِكَ مِنْ أَنۢبَآءِ الْغَيْبِ نُوحِيهِ إِلَيْكَ
وَمَا كُنتَ لَدَيْهِمْ إِذْ يُلْقُونَ أَقْلَٰمَهُمْ أَيُّهُمْ يَكْفُلُ مَرْيَمَ
وَمَا كُنتَ لَدَيْهِمْ إِذْ يَخْتَصِمُونَ ٤٤ إِذْ قَالَتِ الْمَلَٰٓئِكَةُ
يَٰمَرْيَمُ إِنَّ اللَّهَ يُبَشِّرُكِ بِكَلِمَةٍ مِّنْهُ اسْمُهُ الْمَسِيحُ عِيسَى
ابْنُ مَرْيَمَ وَجِيهًا فِي الدُّنْيَا وَالْآخِرَةِ وَمِنَ الْمُقَرَّبِينَ ٤٥



**(38) Yayin da Annabi Zakariyya ya ga irin abin da Allah ya ba Maryam ‘yar Imrana na arziki, wanda ya sava wa al’ada, sai ya yi fatan Allah shi ma ya azurta shi da xa, duk kuwa da halin da yake ciki na tsufa shi da matarsa, ya ce: “Ya Ubangiji, ka ba ni xa nagari. Haqiqa kai mai jin addu’ar wanda ya kiraka ne, mai amsawa ne”.**

**(39) Sai Mala’iku suka kira shi, suka yi masa magana a lokacin yana tsaye yana sallah, a wurin ibadarsa, suka ce: “Haqiqa Allah yana maka bushara da yaro, da za a haifa maka sunansa Yahya. Daga cikin siffofinsa zai zama mai gasgata kalmar Allah – Isa xan Maryam – saboda an halicce shi, halitta ta daban, shi ne da kalmar Allah. Wannan yaron zai zama shugaba ga mutanensa a wajen ilimi da ibada, kuma mai kare kansa da tsare ta daga sha’awa, da kusantar mata, yana mai bautawa Ubangijinsa shi kaxai, kuma zai zama Annabi daga cikin salihan bayi”.**

**(40) Lokacin da Mala’iku suka yi wa Annabi Zakariyya bushara da samun xa, sai ya ce: “Ya Ubangiji ta yaya zan samu xa, bayan na zama tsoho, matata kuma bakarariya ce, ba ta haihuwa?”. Sai Allah ya ba shi amsa da cewa: “Misalin halittar Yahya a lokacin shekarunka da rashin haihuwar matarka, kamar yadda Allah ne yake halittar abin da ya ga dama, daga cikin abin da ya savawa al’ada, saboda Allah mai iko ne akan dukkan komai, yana aikata abin da ya ga dama, da hikimarsa da adalcinsa”.**

**(41) Sai Annabi Zakariyya ya ce: “Ya Ubangiji ka sanya min alama a kan samuwar cikin matata”. Sai Allah ya ce,: “Alamar da ka nema, ita ce, Ka kasa yi wa mutane magana har tsawon kwana uku da darensu, sai dai ka yi nuni da makamancinsa, kuma ba tare da wani abu ya same ka ba, don haka ka yawaita ambaton Allah da tasbihi a farkon rana da qarshenta”.**

**(42) Ka tuna – Ya kai wannan Manzo – yayin da Mala’iku suka cewa Maryam (A.S): “Haqiqa Allah ya zave ki, saboda kyawawan siffofinki na qwarai. Ya tsarkake ki daga tawaya. Ya zave ki a kan matan talikai na zamaninki”.**

**(43) “Ya ke Maryam, ki tsawaita tsayuwa a cikin sallah, ki yi sujjada ga Ubangijinki, ki yi ruku’i tare da masu ruku’u daga cikin bayin Allah salihai”.**

**(44) Wannan abin da aka ambata na labarin Annabi Zakariyya da Maryam (A.S) yana daga cikin labarukan gaibu da muke maka wahayinsu – Ya kai wannan Manzo -. Ba ka tare da waxannan malaman da salihan bayin lokacin da suka yi husuma, a kan wanda ya fi cancanta da tarbiyar Maryam, har sai da suka yi quri’a, suka jefa alqalumansu, sai alqalamin Annabi Zakariyya ya samu nasara.**

**(45) Ka tuna – Ya kai wannan Manzo – lokacin da Mala’iku suka ce: “Ya Maryam! Allah yana miki bushara da yaro, halittarsa zata kasance ba tare da uba ba, sai dai da kalmar Allah, wadda ita ce ya ce: “Kasance” sai yaron ya kasance da izinin Allah. Sunan wannan yaron: Al-Masihu bin Maryam, yana da matsayi babba a duniya da lahira, kuma yana cikin makusanta ga Allah Maxaukakin Sarki”.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kulawar Allah ga waliyyansa. Yana nisantar da su daga mummunan abu, yana amsa addu’o’insu.**

**2 - Falalar Maryam (A.S) ta inda Allah ya zave ta a kan matan talikai, ya tsarkake ta daga tawaya, ya sanya ta mai albarka. 3 - Duk lokacin da ni’imar da Allah ya yi wa bawa ta zama babba, to sai abin da ya wajaba a kansa na godiya ma ya zama babba, ta hanyar tsayuwa a sallah, da ruku’u da sujjada da sauran ibadu.**

**4 - Halaccin yin quri’a yayin da aka yi savani, a cikin abin da babu shaida, kuma babu wata alama da zata nuna abin da ake nema.**

وَيُكَلِّمُ ٱلنَّاسَ فِي ٱلۡمَهۡدِ وَكَهۡلٗا وَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ٤٦
قَالَتۡ رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ لِي وَلَدٞ وَلَمۡ يَمۡسَسۡنِي بَشَرٞۖ قَالَ كَذَٰلِكِ
ٱللَّهُ يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُۚ إِذَا قَضَىٰٓ أَمۡرٗا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ
٤٧ وَيُعَلِّمُهُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَٱلتَّوۡرَىٰةَ وَٱلۡإِنجِيلَ
٤٨ وَرَسُولًا إِلَىٰ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ أَنِّي قَدۡ جِئۡتُكُم بِـَٔايَةٖ مِّن
رَّبِّكُمۡ أَنِّيٓ أَخۡلُقُ لَكُم مِّنَ ٱلطِّينِ كَهَيۡـَٔةِ ٱلطَّيۡرِ فَأَنفُخُ
فِيهِ فَيَكُونُ طَيۡرَۢا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۖ وَأُبۡرِئُ ٱلۡأَكۡمَهَ وَٱلۡأَبۡرَصَ
وَأُحۡيِ ٱلۡمَوۡتَىٰ بِإِذۡنِ ٱللَّهِۖ وَأُنَبِّئُكُم بِمَا تَأۡكُلُونَ وَمَا تَدَّخِرُونَ
فِي بُيُوتِكُمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لَّكُمۡ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٤٩
وَمُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيَّ مِنَ ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَلِأُحِلَّ لَكُم
بَعۡضَ ٱلَّذِي حُرِّمَ عَلَيۡكُمۡۚ وَجِئۡتُكُم بِـَٔايَةٖ مِّن رَّبِّكُمۡ
فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ٥٠ إِنَّ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبُّكُمۡ فَٱعۡبُدُوهُۚ
هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ ٥١ ۞ فَلَمَّآ أَحَسَّ عِيسَىٰ مِنۡهُمُ (نصف الحزب ٦)
ٱلۡكُفۡرَ قَالَ مَنۡ أَنصَارِيٓ إِلَى ٱللَّهِۖ قَالَ ٱلۡحَوَارِيُّونَ نَحۡنُ
أَنصَارُ ٱللَّهِ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَٱشۡهَدۡ بِأَنَّا مُسۡلِمُونَ ٥٢



**(46) Zai yi wa mutane magana yana yaro qarami, tun gabanin ya fara magana, sannan kuma zai musu magana yana babba, a lokacin qarfinsa ya cika. Zai musu magana ne da abin da yake gyaruwar addininsu da rayuwarsu ne. Kuma yana cikin salihan mutane a cikin maganganunsu da ayyukansu.**

**(47) Maryam ta ce, tana mai mamakin ta samu xa ba tare da miji ba: "Ta yaya zai zama ina da xa, alhali wani mutum bai tava kusantata ba, ta hanyar halal ko haram ba?". Sai Mala'ika ya ce da ita, " Kamar yadda Allah ya halitta miki xa ba tare da uba ba, haka yake halittar abin da ya ga dama, daga abubuwan da suka savawa abin da aka sani da al'ada. Idan Allah ya yi nufin wani abu sai ya ce da shi, "Kasance" sai ya kasance, babu abin da yake gagararsa".**

**(48) Zai koya masa littafi da dacewa cikin magana da aiki. Kuma ya koya masa Attaura wadda ya saukar da ita ga Annabi Musa (A.S). Ya koya masa Injila wanda zai saukar masa ita daga baya.**

**(49) Kuma zai sanya shi Manzo zuwa ga Bani Isra'il, zai ce musu: "Ni Manzon Allah ne zuwa gareku, tabbas na zo muku da alamar dake nuna gaskiyar Annabta ta, ita ce,: Zan xauki tavo in suranta tsuntsu kamar yadda yake, in yi busa a cikinsa, kuma sai ya zama tsuntsu mai rai da izinin Allah. Haka nan ina warkar da wanda aka haifa makaho ya zama yana gani, ina warkar da wanda ya gamu da cutar kuturta, fatarsa ta dawo sumul, ina raya wanda yake matacce, amma fa dukkan wannan yana faruwa ne da izinin Allah. Haka nan ina baku labarin abin da kuke ci, da abin da kuke voyewa a gidajenku na abinci. A cikin waxannan abubuwa masu girma da na ambata muku, waxanda xan Adam ba zai iya yin su ba, akwai alama babba a kan cewa ni Manzon Allah ne zuwa gareku, in dai kuna nufin ku yi imani, kuma zaku gasgata hujjoji".**

**(50) Haka nan na zo muku da abin da yake gasgata abin da ya sauka a gabani na, na daga Attaura. Na zo muku don in halatta muku wasu abubuwa da aka haramta muku a baya, don in sauqaqa muku in rangwanta muku. Na zo muku da hujja bayyananniya a kan ingancin abin da na faxa muku. Ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, ku bi ni cikin abin da nake kiranku zuwa gare shi.**

**(51) Duka wannan haka yake, saboda Allah shi ne Ubangijina kuma Ubangijinku, shi ne kaxai wanda ya cancanta a yi wa xa'a, a ji tsoronsa, ku bauta masa shi kaxai, wannan abin da nake umartarku da shi na bautawa Allah da tsoronsa, shi ne tafarki madaidaici, wanda babu karkata a cikinsa.**

**(52) Yayin da Annabi Isa (A.S) ya gane sun ci gaba da kafircinsu. Sai ya ce wa Bani Isra'il: "Waye zai taimake ni a wajen da'awa zuwa ga Allah?" Sai zavavvun mabiyansa suka ce: "Mu ne mataimaka addinin Allah, mun yi imani da Allah, mun bi ka, ka shaida – Ya kai Isa – mu, masu miqa wuya ne ga Allah da kaxaita shi, da yi masa biyayya.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Nuna darajar rubutu da zane, ta yadda Allah ya fara da su, kafin waninsu.**

**2 - Yana daga cikin sunnonin Allah ya qarfafa Manzanninsa da ayoyin da suke nuna gaskiyarsu, irin ayoyin da mutum ba zai iya ba.**

**3 - Annabi Isa (A.S) ya zo da sauwaqawa ga Bani Isra'il cikin abin da aka tsananta musu a cikin wasu shari'o'in da suke cikin Attaura. Wannan dalili ne da yake nuna ana samun shafe hukunci a cikin shari'un da suka gabata.**

رَبَّنَآ ءَامَنَّا بِمَآ أَنزَلۡتَ وَٱتَّبَعۡنَا ٱلرَّسُولَ فَٱكۡتُبۡنَا مَعَ
ٱلشَّٰهِدِينَ ٥٣ وَمَكَرُواْ وَمَكَرَ ٱللَّهُۖ وَٱللَّهُ خَيۡرُ ٱلۡمَٰكِرِينَ
٥٤ إِذۡ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَىٰٓ إِنِّي مُتَوَفِّيكَ وَرَافِعُكَ إِلَيَّ وَمُطَهِّرُكَ
مِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَجَاعِلُ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوكَ فَوۡقَ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوٓاْ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِۖ ثُمَّ إِلَيَّ مَرۡجِعُكُمۡ فَأَحۡكُمُ
بَيۡنَكُمۡ فِيمَا كُنتُمۡ فِيهِ تَخۡتَلِفُونَ ٥٥ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
فَأُعَذِّبُهُمۡ عَذَابٗا شَدِيدٗا فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ وَمَا لَهُم
مِّن نَّٰصِرِينَ ٥٦ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
فَيُوَفِّيهِمۡ أُجُورَهُمۡۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ٥٧ ذَٰلِكَ نَتۡلُوهُ
عَلَيۡكَ مِنَ ٱلۡأٓيَٰتِ وَٱلذِّكۡرِ ٱلۡحَكِيمِ ٥٨ إِنَّ مَثَلَ
عِيسَىٰ عِندَ ٱللَّهِ كَمَثَلِ ءَادَمَۖ خَلَقَهُۥ مِن تُرَابٖ ثُمَّ قَالَ لَهُۥ
كُن فَيَكُونُ ٥٩ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُن مِّنَ ٱلۡمُمۡتَرِينَ
٦٠ فَمَنۡ حَآجَّكَ فِيهِ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَكَ مِنَ ٱلۡعِلۡمِ فَقُلۡ تَعَالَوۡاْ
نَدۡعُ أَبۡنَآءَنَا وَأَبۡنَآءَكُمۡ وَنِسَآءَنَا وَنِسَآءَكُمۡ وَأَنفُسَنَا
وَأَنفُسَكُمۡ ثُمَّ نَبۡتَهِلۡ فَنَجۡعَل لَّعۡنَتَ ٱللَّهِ عَلَى ٱلۡكَٰذِبِينَ ٦١



**(53) Zavavvun mabiya Annabi Isa (wato Hawariyawa) suka ci gaba da cewa: "Ya Ubangijinmu mun yi imani da abin da ka saukar na Injila. Mun bi Annabi Isa (A.S). Ka sa mu cikin waxanda suka shaida da gaskiya, waxanda suka yi imani da kai da Manzanninka".**

**(54) Kafirai daga cikin Bani Isra'il sun yi makircin qoqarin kashe Annabi Isa (A.S), don haka sai Allah ya mayar musu da makircinsu, ya bar su a cikin vatansu. Ya sa kamannin Annabi Isa a jikin wani mutum. Allah Shi ne mafi alherin mai mayar da makirci zuwa ga masu yin sa, kuma ba wani makirci da ya fi tsanani fiye da na Allah ga maqiyansa.**

**(55) Allah ya mayar musu da makircinsu, yayin da ya ce da Annabi Isa (A.S): "Ya Isa zan dawo da kai wajena, amma ba da mutuwa ba, zan xaukaka jikinka da ruhinka zuwa gare ni, in tsarkake ka daga qazantar waxanda suka kafirce maka, suka yi nisa da kai. Zan sanya waxanda suka bi ka a kan addinin gaskiya – wanda daga cikinsa akwai imani da Annabi Muhammad (S.A.W) – sama da waxanda suka kafirce maka wajen hujja, har zuwa ranar alqiyama, in yi hukuncin gaskiya tsakaninku cikin abin da kuke yin savani.**

**(56) Waxanda suka kafirce da kai, da gaskiyar da ka zo musu da ita, sai in azabtar da su azaba mai tsanani a duniya, ta hanyar kisa da kamu da qasqanci da waninsu. A lahira kuma in azabtar da su da wuta, sannan kuma ba su da mataimaka waxanda za su kare su daga azaba.**

**(57) Amma waxanda suka yi imani da kai, da gaskiyar da ka zo musu da ita, suka yi ayyuka nagari, daga sallah da azumi da sada zumunci da sauransu, to haqiqa Allah zai ba su ladan ayyukansu cikakke, ba za a tauye masu komai ba.**
**Wannan bayani ne a kan mabiya Almasihu (wato Annabi Isa) tun gabanin aiko Annabi Muhammad (S.A.W) wanda ya yi bushara da zuwan Almasihu kansa. Allah ba ya son Azzalumai, wanda yana daga mafi girman zalunci shirka da Allah da qaryata Manzanninsa.**

**(58) Wannan abin da muke karanta maka na labarin Annabi Isa (A.S) yana daga cikin alamomi bayyanannu da suke nuna ingancin abin da aka saukar maka, wanda tunatarwa ne ga masu tsoron Allah, kuma abu tsararre, varna ba ta zuwar masa ta ko'ina.**

**(59) Misalin halittar Annabi Isa (A.S) a wurin Allah, kamar misalin halittar Annabi Adamu ce daga turvaya, ba tare da uba da uwa ba, kaxai Allah ya ce masa ne, "Zama mutum", sai ya zama, kamar yadda Allah ya yi nufi, to ta yaya za su riqa riya cewa Annabi Isa Allah ne, suna kafa hujjar cewa an halicce shi ba tare da Uba ba, alhali suna tabbatar da Annabi Adamu mutum ne, duk da an halicce shi, ba uwa ba uba!.**

**(60) Gaskiyar da ba shakka a cikinta dangane da Annabi Isa (A.S) ita ce abin da aka saukar maka daga Ubangijinka, don haka kada ka kasance daga cikin masu shakka, masu kokanto, ka tabbata a kan abin da kake kai na gaskiya.**

**(61) Duk wanda ya yi jayayya da kai – Ya kai wannan Annabi – daga cikin Nasaran garin Najran a kan lamarin Annabi Isa, wanda suke riya cewa, shi ba bawan Allah ba ne, bayan abin da ya zo maka na ingantaccen ilimi a kan sha'aninsa, to ka ce musu: "Ku zo mu kira 'ya'yanmu da 'ya'yanku, da matanmu da matanku, da mu kanmu, da ku kanku, mu haxu gaba xaya, sannan mu qanqantar da kai ga Allah da addu'a, a kan ya saukar da tsinuwarsa a kan maqaryata a cikinmu, mu da ku.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Yana daga cikin cikar ikon Allah Maxaukakin Sarki yin uquba ga wanda yake wa addininsa da waliyyansa makirci, sai ya mayar musu da makircinsu kamar yadda suka yi. 2 - Bayanin ingantacciyar aqida dangane da sha'anin Annabi Isa (A.S) da dacewarta da hankali, don ba shi ne na farko a cikin halittar Allah ba. Annabi Adamu an halicce shi ba ba uwa ba uba, abu mai tsananin ban mamaki, amma kuma kowa ya yarda cewa shi mutum ne ba Allah ba ne. 3 - Shar'ancin yin Mubahala (Tsinuwa) a tsakanin masu savani, kamar yadda wannan ayar mai girma ta zo da ita.**

إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ ٱلْقَصَصُ ٱلْحَقُّ ۚ وَمَا مِنْ إِلَٰهٍ إِلَّا ٱللَّهُ ۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ
ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ٦٢ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِٱلْمُفْسِدِينَ
٦٣ قُلْ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ تَعَالَوْا۟ إِلَىٰ كَلِمَةٍ سَوَآءٍۭ بَيْنَنَا
وَبَيْنَكُمْ أَلَّا نَعْبُدَ إِلَّا ٱللَّهَ وَلَا نُشْرِكَ بِهِۦ شَيْـًٔا وَلَا يَتَّخِذَ
بَعْضُنَا بَعْضًا أَرْبَابًا مِّن دُونِ ٱللَّهِ ۚ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَقُولُوا۟ ٱشْهَدُوا۟
بِأَنَّا مُسْلِمُونَ ٦٤ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ لِمَ تُحَآجُّونَ فِىٓ إِبْرَٰهِيمَ
وَمَآ أُنزِلَتِ ٱلتَّوْرَىٰةُ وَٱلْإِنجِيلُ إِلَّا مِنۢ بَعْدِهِۦٓ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ
٦٥ هَٰٓأَنتُمْ هَٰٓؤُلَآءِ حَٰجَجْتُمْ فِيمَا لَكُم بِهِۦ عِلْمٌ فَلِمَ
تُحَآجُّونَ فِيمَا لَيْسَ لَكُم بِهِۦ عِلْمٌ ۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ
لَا تَعْلَمُونَ ٦٦ مَا كَانَ إِبْرَٰهِيمُ يَهُودِيًّا وَلَا نَصْرَانِيًّا
وَلَٰكِن كَانَ حَنِيفًا مُّسْلِمًا وَمَا كَانَ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ٦٧
إِنَّ أَوْلَى ٱلنَّاسِ بِإِبْرَٰهِيمَ لَلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُ وَهَٰذَا ٱلنَّبِىُّ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ ۗ وَٱللَّهُ وَلِىُّ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٦٨ وَدَّت طَّآئِفَةٌ مِّنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ
لَوْ يُضِلُّونَكُمْ وَمَا يُضِلُّونَ إِلَّآ أَنفُسَهُمْ وَمَا يَشْعُرُونَ ٦٩ يَٰٓأَهْلَ
ٱلْكِتَٰبِ لِمَ تَكْفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَأَنتُمْ تَشْهَدُونَ ٧٠



**(62) Wannan abin da muka faxa maka dangane da sha'anin Annabi Isa (A.S) shi ne labarin gaskiya wanda ba qarya ko shakka a cikinsa. Babu wani abin bautawa da gaskiya da cancanta sai Allah shi kaxai. Haqiqa Allah Mabuwayi ne a cikin mulkinsa, mai hikima ne a cikin tsarinsa da lamarinsa da halittarsa.**

**(63) Idan suka bijire daga abin da ka zo da shi, suka qi bin ka, to wannan yana cikin vacewarsu. Allah yana sane da mavarnata a bayan qasa, zai kuma saka musu a kan haka.**

**(64) Ka ce – Ya kai wannan Manzo – ku zo ya ku Ma'abota littafi daga Yahudu da Nasara, mu haxu a kan kalmar adalci, wadda za mu daidaita a cikinta gaba xaya, ita ce, mu kaxaita Allah da ibada, kada mu bautawa kowa tare da shi, ko mene ne matsayinsa, kowace irin martaba ya kai, sannan kada sashenku ya riqi sashe abun bautawa, yana musu xa'a koma bayan Allah. Idan suka juya baya daga wannan abin da kake kiransu zuwa gare shi na gaskiya da adalci, to yaku Muminai ku ce musu: "Ku shaida, mu mun miqa wuya ga Allah, mun jayu zuwa gare shi Maxaukakin Sarki da yi masa xa'a".**

**(65) Yaku Ma'abota littafi don me kuke jayayya a cikin addinin Annabi Ibrahim (A.S) Bayahude yana riya cewa Annabi Ibrahim Bayahude ne. shi ma Nasara yana riya cewa Annabi Ibrahim nasara ne, alhali kun san cewa yahudanci da kiristanci ba su bayyana ba sai bayan mutuwarsa da lokaci mai tsawo. Yanzu ba kwa gane vacin maganarku da kuskuren abin da kuke rayawa da hankulanku. (66) Ga ku nan ku – Ma'abota littafi – kun yi jayayya da Annabi (S.A.W) a kan abin da kuke da ilimi na daga al'amarin addininku da abin da aka saukar muku, to kuma don me kuke jayayya a kan abin da baku da ilimi na daga al'amarin Annabi Ibrahim da addininku? Daga abin da baya cikin littafanku, kuma Annabawanku ba su zo da shi ba?! Allah ya san haqiqanin al'amura da voyayyunsu, amma ku baku sani ba. (67) Annabi Ibrahim bai kasance a kan addinin yahudanci, ko addinin kiristanci ba, shi dai ya kasance mai karkata ne ga barin vatattun addinai, mai sallamawa ne ga Allah shi kaxai Maxaukaki, kuma ba ya cikin masu yin shirka da Allah, kamar yadda mushirikan larabawa suke zato cewa yana kan addininsu.**

**(68) Waxanda suka fi dukkan mutane cancantar dangantuwa ga Annabi Ibrahim su ne waxanda suka bi abin da ya zo da shi a zamaninsa. Hakanan waxanda suka fi cancanta da shi, su ne wannan Annabi, wato Annabi Muhammad (S.A.W) da waxanda suka yi imani daga cikin wannan al'umma. Allah mai taimakon waxanda suka yi imani da shi ne, kuma mai kare su.**

**(69) Malamai ma'abota littafi daga cikin Yahudu da Nasara sun yi burin a ce sun vatar da ku – yaku muminai – ga barin gaskiyar da Allah ya shiryar da ku zuwa gare ta, amma ba kowa suke vatarwa ba sai kawunansu, saboda qoqarinsu na vatar da muminai yana qara vatar da su ne, kuma ba su san qarshen aikinsu ba.**

**(70) Ya ku Ma'abota littafi, Yahudu da Nasara don me kuke kafirce wa ayoyin Allah waxanda ya saukar muku, da abin da yake cikinsu na dalilai a kan Annabtar Muhammad (S.A.W), alhali kuna shaidawa shi ne gaskiyar da littafanku suka nuna.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Dukkan saqonnin da Allah ya aiko sun haxu a kan kalmar adalci, ita ce, kaxaita Allah Maxaukakin Sarki da hana shirka. 2 - Mahimmancin sanin tarihi, saboda yana iya zama cikin hujjoji masu qarfi da suke mayar da da'awar mavarnata. 3 - Wanda ya fi dukkan mutane cancanta da Annabi Ibrahim shi ne wanda yake kan addininsa da aqidarsa. Amma da'awar dangantuwa zuwa gare shi tare da sava masa, wannan ba ya da amfani. 4 - Ayoyin sun nuna irin yadda kafirai ma'abota littafi suke kwaxayin vatar da muminai daga cikin wannan al'umma, saboda hassadar da take cikin zukatansu.**

يَا أَهْلَ الْكِتَابِ لِمَ تَلْبِسُونَ الْحَقَّ بِالْبَاطِلِ وَتَكْتُمُونَ الْحَقَّ
وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ٧١ وَقَالَت طَّائِفَةٌ مِّنْ أَهْلِ الْكِتَابِ آمِنُوا
بِالَّذِي أُنزِلَ عَلَى الَّذِينَ آمَنُوا وَجْهَ النَّهَارِ وَاكْفُرُوا آخِرَهُ
لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ٧٢ وَلَا تُؤْمِنُوا إِلَّا لِمَن تَبِعَ دِينَكُمْ قُلْ إِنَّ
الْهُدَىٰ هُدَى اللَّهِ أَن يُؤْتَىٰ أَحَدٌ مِّثْلَ مَا أُوتِيتُمْ أَوْ يُحَاجُّوكُمْ
عِندَ رَبِّكُمْ ۗ قُلْ إِنَّ الْفَضْلَ بِيَدِ اللَّهِ يُؤْتِيهِ مَن يَشَاءُ ۗ وَاللَّهُ
وَاسِعٌ عَلِيمٌ ٧٣ يَخْتَصُّ بِرَحْمَتِهِ مَن يَشَاءُ ۗ وَاللَّهُ ذُو الْفَضْلِ
علامة ربع الحزب ٦ الْعَظِيمِ ٧٤ ۞ وَمِنْ أَهْلِ الْكِتَابِ مَنْ إِن تَأْمَنْهُ بِقِنطَارٍ
يُؤَدِّهِ إِلَيْكَ وَمِنْهُم مَّنْ إِن تَأْمَنْهُ بِدِينَارٍ لَّا يُؤَدِّهِ إِلَيْكَ
إِلَّا مَا دُمْتَ عَلَيْهِ قَائِمًا ۗ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَالُوا لَيْسَ عَلَيْنَا فِي
الْأُمِّيِّينَ سَبِيلٌ وَيَقُولُونَ عَلَى اللَّهِ الْكَذِبَ وَهُمْ يَعْلَمُونَ
٧٥ بَلَىٰ مَنْ أَوْفَىٰ بِعَهْدِهِ وَاتَّقَىٰ فَإِنَّ اللَّهَ يُحِبُّ الْمُتَّقِينَ
٧٦ إِنَّ الَّذِينَ يَشْتَرُونَ بِعَهْدِ اللَّهِ وَأَيْمَانِهِمْ ثَمَنًا قَلِيلًا
أُولَٰئِكَ لَا خَلَاقَ لَهُمْ فِي الْآخِرَةِ وَلَا يُكَلِّمُهُمُ اللَّهُ وَلَا يَنظُرُ
إِلَيْهِمْ يَوْمَ الْقِيَامَةِ وَلَا يُزَكِّيهِمْ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ٧٧



**(71) Ya Ma'abota littafi don me kuke cakuxa gaskiyar da aka saukar muku a littafanku da varnar da take daga wurinku. Kuna voye abin da yake cikinsu na gaskiya da shiriya, wanda daga cikinsa akwai Anabcin Muhammad (S.A.W), alhali kun san gaskiya da varna, kun san shiriya da vata.**

**(72) Wasu jama'a daga cikin malaman Yahudu suka ce: "Ku yi imani a zahiri da wannan Alqur'anin da aka saukar wa muminai a farkon rana, a qarshen yini sai ku kafirce da shi, ko hakan ya sa su yi shakka a cikin addininsu saboda kun kafirce masa bayan da kun yi imani da shi", su ma sai su bar shi, suna masu cewa: Ai su sun fi mu sanin littafan Allah amma ga shi sun dawo daga imani da shi.**

**(73) Suka sake cewa: "Kada ku yi imani, ku bi kowa sai wanda ya zama yana bin addininku". To ka ce musu – Ya kai wannan Manzo – shiriya zuwa ga gaskiya, ita ce shiriyar Allah Maxaukakin Sarki, ba abin da kuke kai ba na qarya da taurin kai, saboda tsoron kada aba wani irin falalar da aka ba ku, ko kuma don tsoron kada su yi muku hujja da shi a wajen Ubangijinku, yayin da kuka tabbatar da an saukar musu". To ka faxa musu – Ya kai wannan Manzo – falala tana hannun Allah yana bawa wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, falalarsa ba ta taqaitu a kan wata al'umma ba, banda wata ba. Allah mai yalwar falala ne, ya kuma san wanda ya cancance ta.**

**(74) Yana keve wanda ya so da rahamarsa daga cikin halittarsa, ya yi masa falala da shiriya da Annabta da sauran kyautuka. Allah Ma'abocin falala ce mai girma, wadda ba ta da iyaka.**

**(75) Daga cikin Ahlul- Kitabi akwai wanda in ka amince masa da dukiya mai yawa, zai dawo maka da abin da ka amince masa da shi. Daga cikinsu akwai wanda in ka amince masa a kan dukiya kaxan, ba zai dawo maka da abin da ka amince masa ba, sai dai in ka tsaya a kansa, ka yi nacin neman ya biya ka, saboda zatonsu da maganarsu da suke cewa: "Babu laifi a kanmu cikin duk abin da muka yi wa larabawa, ko muka ci dukiyarsu, saboda Allah ya halatta mana ita", suna faxar wannan qaryar alhali suna sane da qaryar da suke yi wa Allah.**

**(76) Lamarin ba kamar yadda suka riya ba ne, suna da laifi, sai dai wanda ya cika alqawarin da ya yi wa Allah, na imani da shi, da Manzanninsa, ya cika alqawarin da yake tsakaninsa da mutane, ya bayar da amana, ya ji tsoron Allah da kamanta bin umarninsa da nisantar abubuwan da ya hana. Haqiqa Allah yana son masu tsoronsa, zai kuma saka musu da mafi girman sakamako a kan haka.**

**(77) Waxanda suke canza wasiyyar Allah da ya yi musu, ta bin abin da ya saukar a littafinsa, ya aiko Manzanninsa da shi, suka canza rantse-rantsensu da suka yi na cika alqawarin da suka xauka ga Allah, suka canza shi da wani abu kaxan na jin daxin duniya, to ba su da rabo daga ladan lahira, Allah ba zai musu maganar da zata faranta musu rai ba, ba zai kalle su, kallo na rahama ba ranar alqiyama, suna da azaba mai raxaxi.**

## ۞ Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Daga cikin malaman Ma'abota littafi akwai waxanda suke yaudarar masu bin addininsu, ba sa bayyana musu gaskiyar da littafansu suka nuna musu, kuma Manzanninsu suka zo da ita.**

**2 - Yana daga cikin hanyoyin da kafirai suke bi, shiga cikin addini da sanya shakka a cikinsa.**

**3 - Allah Maxaukakin Sarki shi ne mai falala mai bayarwa, yana ba wanda ya ga dama daga falalarsa, yana hana wanda ya ga dama da adalcinsa da hikimarsa, ba a kuma samun falalarsa sai da yi masa biyayya.**

**4 - Duk wani abu da za a samu a maimakon imani da Allah da cika alqawarinsa – komai girman abun – to qasqantacce ne, wulaqantacce ne idan aka haxa shi da ladan lahira da masaukanta.**

وَإِنَّ مِنْهُمْ لَفَرِيقًا يَلْوُۥنَ أَلْسِنَتَهُم بِٱلْكِتَـٰبِ لِتَحْسَبُوهُ
مِنَ ٱلْكِتَـٰبِ وَمَا هُوَ مِنَ ٱلْكِتَـٰبِ وَيَقُولُونَ هُوَ مِنْ
عِندِ ٱللَّهِ وَمَا هُوَ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ وَيَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ
وَهُمْ يَعْلَمُونَ ﴿٧٨﴾ مَا كَانَ لِبَشَرٍ أَن يُؤْتِيَهُ ٱللَّهُ ٱلْكِتَـٰبَ
وَٱلْحُكْمَ وَٱلنُّبُوَّةَ ثُمَّ يَقُولَ لِلنَّاسِ كُونُوا۟ عِبَادًا لِّى مِن
دُونِ ٱللَّهِ وَلَـٰكِن كُونُوا۟ رَبَّـٰنِيِّـۧنَ بِمَا كُنتُمْ تُعَلِّمُونَ
ٱلْكِتَـٰبَ وَبِمَا كُنتُمْ تَدْرُسُونَ ﴿٧٩﴾ وَلَا يَأْمُرَكُمْ أَن
تَتَّخِذُوا۟ ٱلْمَلَـٰٓئِكَةَ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ أَرْبَابًا ۗ أَيَأْمُرُكُم بِٱلْكُفْرِ بَعْدَ
إِذْ أَنتُم مُّسْلِمُونَ ﴿٨٠﴾ وَإِذْ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَـٰقَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ لَمَآ ءَاتَيْتُكُم
مِّن كِتَـٰبٍ وَحِكْمَةٍ ثُمَّ جَآءَكُمْ رَسُولٌ مُّصَدِّقٌ لِّمَا
مَعَكُمْ لَتُؤْمِنُنَّ بِهِۦ وَلَتَنصُرُنَّهُۥ ۚ قَالَ ءَأَقْرَرْتُمْ وَأَخَذْتُمْ
عَلَىٰ ذَٰلِكُمْ إِصْرِى ۖ قَالُوٓا۟ أَقْرَرْنَا ۚ قَالَ فَٱشْهَدُوا۟ وَأَنَا۠ مَعَكُم
مِّنَ ٱلشَّـٰهِدِينَ ﴿٨١﴾ فَمَن تَوَلَّىٰ بَعْدَ ذَٰلِكَ فَأُو۟لَـٰٓئِكَ هُمُ
ٱلْفَـٰسِقُونَ ﴿٨٢﴾ أَفَغَيْرَ دِينِ ٱللَّهِ يَبْغُونَ وَلَهُۥٓ أَسْلَمَ مَن فِى
ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ طَوْعًا وَكَرْهًا وَإِلَيْهِ يُرْجَعُونَ ﴿٨٣﴾



**(78) Daga cikin Yahudawa akwai wasu jama'a da suke juyar da harshensu wajen faxin abin da baya cikin Attaurar da aka saukar daga wajen Allah, saboda ku yi zaton suna karanta Attaura, amma ba daga Attaura ba ne, qaryarsu ce da qirqire-qirqirensu ga Allah. Suna kuma cewa: "Abin da muke karantawa, Allah ne ya saukar da shi", amma fa ba daga Allah yake ba, suna yi wa Allah qarya alhali suna sane da qarya suke wa Allah da Manzanninsa.**

**(79) Bai dace da mutum ba, Allah ya ba shi littafin da ya saukar daga wajensa, ya kuma azurta shi da ilimi da fahimta, ya zave shi a matsayin Annabi, sannan ya cewa mutane: "Ku zama bayina koma bayan Allah". Sai dai zai ce musu ne: "Ku zama malamai masu aiki da iliminsu, masu renon mutane, masu gyara al'amuransu, saboda koyawa mutane littafin da aka saukar da kuke yi, da kuma abin da kuke karantawa da hardacewa da fahimta daga cikinsa".**

**(80) Haka nan baya dacewa da shi ya umarce ku ku riqi Mala'iku da Annabawa abubuwan bauta, kuna bauta musu koma bayan Allah. Shin zai halatta a gare shi ya umarce ku da kafirce wa Allah bayan kun miqa wuya, kun sallama gare shi?!.**

**(81) Ka tuna – Ya kai wannan Manzo – yayin da Allah ya riqi alqawari mai qarfi a wajen Annabawa, ya ce musu: "Duk irin abin da na baku na littafin da zan saukar muku, ko hikima da zan koya muku, kuma kowane matsayi xayanku zai kai, sai Manzo ya zo muku daga wajena – Shi ne Annabi Muhammad (S.A.W) – yana mai gasgata abin da yake wajenku na littafi da hikima, to zaku yi imani da abin da ya zo da shi, kuma zaku taimake shi, ku bi shi. Shin kun yarda da haka – Ya ku Annabawa -?, kuma kun xau alqawari mai tsanani a kan haka? Sai suka amsa da cewa: "Mun yarda". Allah ya ce: "To ku shaida, haka ma al'ummunku su shaida, ni ma ina tare da ku cikin masu shaidawa".**

**(82) Waxanda suka bijire bayan wannan alqawari mai qarfi da aka yi da su, to waxannan su ne waxanda suka fita daga addinin Allah da xa'arsa.**

**(83) Yanzu wanin addinin musulunci wanda Allah ya zavar wa bayinsa, waxanda suka bar addinin Allah suke nema? Alhali halittun da suke sammai da qassai ga Allah suka miqa wuya, a halin suna so - kamar halin muminai - ko basa so - kamar halin kafirai - Sannan zuwa ga Allah dukka halittu za su koma ranar alqiyama don yin hisabi da bada sakamako.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tabbatar da vatan malaman Yahudu da makircinsu da canzawarsu ga zancen Allah, da qaryar da suke yi wa mutane, suna cewa canzawar daga Allah ne.**

**2 - Duk wanda yake da'awar bin addinin wani daga cikin Annabawan Allah, idan bai yi imani da Annabi Muhammad ba (S.A.W) ba, to ya warware alqawarinsa da Allah Maxaukakin Sarki.**

**3 - Waxanda suka fi dukkan mutane matsayi sune malamai na Allah, waxanda suka haxa tsakanin ilimi da aiki, kuma suke renon mutane a kai.**

**4 - Mafi girman vata shi ne bijirewa addinin Allah, tsarki ya tabbata a gare shi, wanda dukkan halittu suka sallama masa, nagarinsu da fajiransu.**

قُلۡ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ عَلَيۡنَا وَمَآ أُنزِلَ عَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ
وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَمَآ أُوتِيَ مُوسَىٰ
وَعِيسَىٰ وَٱلنَّبِيُّونَ مِن رَّبِّهِمۡ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّنۡهُمۡ
وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ٨٤ وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن
يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٨٥ كَيۡفَ
يَهۡدِي ٱللَّهُ قَوۡمٗا كَفَرُواْ بَعۡدَ إِيمَٰنِهِمۡ وَشَهِدُوٓاْ أَنَّ
ٱلرَّسُولَ حَقّٞ وَجَآءَهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُۚ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ
ٱلظَّٰلِمِينَ ٨٦ أُوْلَٰٓئِكَ جَزَآؤُهُمۡ أَنَّ عَلَيۡهِمۡ لَعۡنَةَ ٱللَّهِ
وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلنَّاسِ أَجۡمَعِينَ ٨٧ خَٰلِدِينَ فِيهَا لَا يُخَفَّفُ
عَنۡهُمُ ٱلۡعَذَابُ وَلَا هُمۡ يُنظَرُونَ ٨٨ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُواْ مِنۢ
بَعۡدِ ذَٰلِكَ وَأَصۡلَحُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٌ ٨٩ إِنَّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ بَعۡدَ إِيمَٰنِهِمۡ ثُمَّ ٱزۡدَادُواْ كُفۡرٗا لَّن تُقۡبَلَ تَوۡبَتُهُمۡ
وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلضَّآلُّونَ ٩٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَمَاتُواْ وَهُمۡ
كُفَّارٞ فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡ أَحَدِهِم مِّلۡءُ ٱلۡأَرۡضِ ذَهَبٗا وَلَوِ
ٱفۡتَدَىٰ بِهِۦٓۗ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ٩١



**(84) Ka ce – Ya kai Wannan Manzo – mun yi imani da Allah abin bautawa, mun bi shi a cikin abin da ya umarce mu, mun yi imani da wahayin da aka saukar mana, da wanda aka saukar wa Annabi Ibrahim da Annabi Isma'il da Annabi Ishaq da Annabi Ya'aqub, da abin da aka saukar wa Annabawa daga cikin 'ya'yan Annabi Ya'aqub, da abin da aka bawa Annabi Musa da Annabi Isa da Annabawa gaba xaya na daga littattafai da ayoyi daga Ubangijinsu, ba ma rarrabewa a tsakaninsu, mu yarda da wasu, mu kafirce wa wasu. Mun miqa wuya ga Allah shi kaxai, mun sallama masa Maxaukakin Sarki.**

**(85) Duk wanda ya nemi wani addini ba addinin da Allah ya yarda da shi ba, wanda shi ne addinin musulunci, to ba za a karva daga gare shi ba, kuma shi a lahira yana cikin waxanda suka yi hasarar kawunansu, saboda shigar su wuta.**

**(86) Ta yaya Allah zai datar da mutane zuwa ga imani da shi da Manzonsa, alhali sun kafirce bayan imaninsu da Allah, da shaidawarsu a kan abin da Manzon Allah Muhammad (S.A.W) ya zo da shi gaskiya ne, hujjoji bayyanannu a kan ingancin haka sun zo musu. Allah ba ya datar da mutane azzalumai waxanda suka zavi vata bayan shiriya ta zo musu zuwa ga imani da shi.**

**(87) Haqiqa sakamakon waxannan azzalumai waxanda suka zavi vata shi ne tsinuwar Allah da ta Mala'iku da mutane gaba xaya ta tabbata a kansu. Su abin nesantarwa ne daga rahamar Allah.**

**(88) Suna masu dauwama a cikin wuta, ba za su fita daga cikinta ba, kuma ba za a saukaka musu azabarta ba, kuma ba za a jinkirta musu don su tuba su bada uzuri ba.**

**(89) Sai dai waxanda suka koma ga Allah bayan kafircinsu da zaluncinsu, suka gyara ayyukansu, to haqiqa Allah mai gafara ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa, mai jin qan su ne.**

**(90) Waxanda suka kafirta bayan sun yi imani, kuma suka zarce a kan kafircinsu har suka mutu, to ba za a karvi tubansu ba yayin da mutuwa ta zo musu, saboda lokacin tuban ya wuce. Kuma waxannan su ne waxanda suka vace daga tafarki madaidaici, wanda yake isar wa zuwa ga Allah Maxaukakin Sarki.**

**(91) Waxanda suka kafirta, suka mutu a kan kafircinsu, ba za a karvi cikin qasa na zinare ba daga wurinsu, idan sun bayar da shi don a raba su daga wuta. Suna da azaba mai raxaxi, kuma ba su da wasu mataimaka ranar alqiyama da za su kare musu azaba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Wajibi ne yin imani da dukkan Annabawan da Allah ya aiko, da dukkan littafan da ya saukar musu, ba tare da rarrabewa ba.**

**2 - Allah ba zai karvi kowane addini ba daga wurin wani, bayan aiko Annabi Muhammad (S.A.W) sai addinin musulunci, wanda Manzon Allah ya zo da shi.**

**3 - Duk wanda ya zarce a kan vata, ya ci gaba da yin shi, to Allah zai masa uquba da rashin datar da shi zuwa ga tuba da shiriya.**

**4 - Qofar tuba a buxe take ga bawa, matuqar mutuwa ba ta zo masa ba, ko rana ba ta vullo daga mafarxarta ba, a wannan lokaci ba za a karvi tubansa ba.**

**5 - Babu abin da zai tseratar da mutum daga azaba ranar alqiyama sai aikinsa na qwarai. Dukiya ko da ta kai cikin qasa ba zata amfana masa da komai ba.**